IDAN RANA TA FITO 3

1 Daf da magariba zanshiga gida baba yace jidda daga ina nace bab ce ta aikeni karbomata kudin adashi to canjimawa kizo inane manki to baba nashiga gidan nakaimata kudin nayi alwala nayi sallah nazo ina raragefan karbar abincina duk daninayi sunatahirarsu bancemusu sunyi sallarba baba gaje tadubeni rabe raben ubanme kikeyi nace tuwona tadaga murya shegiya uwarcintsiya to hinduwa tazonabata naki nayishiru inakallon hindan tana yanka loma hinden tace tashi akanmu kinzuramin ido karkisa nakware babagaje tace kurwarta kur yar mayu itada abinda kecikinta nakoma jikin dakinazauna yunwa nakeji sosai don yaukoda rana banci abinciba duk dadai dama bakullun nakesamu incisau ukuba inananzaune nakifa kaina cikin cinyata har baba yaleko yace gaje akawomin abincina ga mamakina sainaji shimatace hinduwa tacinye
2 nadago inadubansu cikin mamakin abincin da ta kauda yajuya batare dayace komaiba yasaba dama shinezai kawo adafa ahanashi namikezan fita gidan ubanwa zakikuma tadakan tsawa zandauko kofin ruwan babane indibo masa wani aifagara kusha ruwan kukwanta nayi sallama dakin baba yana zaune yakunna yarfitilarsa acibaibai nadauki kofin taredacewa baba bari nadebo maka ruwansha yaceto dana dawo da ruwa na ajemasa yace kinci abinci ne nace a a nawa da naka duka hinduwa tacinye yagirgiza kai cikin takaici tozokije kisayo mana rake da rogo idama za asamu wannan mai naman dakezuwa daga garako dakinsayo manamunci nazauna sosai inadubansa baba kudi kasamune yayi dan murmushi jekidawo dandali naje babu mainama saime kifi nasayomana darake da rogo nadawo baba yaje salla nasamu guri nazauna dan innashiga baba bazata barni infitoba duk dahaka sada tafito
3..Na dago ina dubansu cikin mmkn abincin da ta kauda ya juya ba tare da ya ce komaiba.Ya saba dama shi ne za ya kawo ayi kuma a hana shi. Na mike zan fita."Gidan uban wa za ki je kuma?" Ta dakan tsawa.""Zan dauko kofin ruwan Baba ne in dibar masa wani.""Ai fa gara ku sha ruwan ku kwanta."Na yi sallama dakin Baba, yana zaune ya kunna 'yar fitilarsa aci bal-bal. Nadauki kofin tare da cewa,"Baba bari na dibo maka ruwan sha." Ya ce,"To." Da na dawo da ruwan na aje masa ya ce,"Kin ci abinci ne?" Na ce," "A'a nawa da naka dukaHinde ta cinye.Ya girgiza kai cikin takaici."To zo ki je ki sayo mana rake da rago.In dama za a samu wannan mai naman da kezuwa daga Garko da kin sayo mana mun ci."Na zauna sosai ina duban shi."Baba Kudi ka samu ne?"Ya yi dan murmushi."Je ki dawo.Dandali naje babu mai nama sai mai kifi, na sayo mana da rake da rogo na dawo. Baba ya je sallah.Nasamu guri na zauna don in na shiga gida Baba ba zata bari in fito ba, duk da haka sai da ta fito tana kwala min kira."Ke Kuluwa gidan uban wa ki ka shiga?"Na fito da sauri daga shagon Baba don kada ta shigo taga abin da na siyo, na ce mata"Baba ne ya ce in tsare mSep 3Aisha Ummu Shureim Sa'eedMsmart BG Zee Town3.Tsaki taja tare da cewa."Dakin banzan shi in dai ya dawo ki zo ki gyara wa Hinduwa makwanci, saura daga nan ki tafi kula mazan naki."Lkcn da Baba ya dawo, na bashi sakon ya ce na zauna muci amma shi ba zaya ci kafin ba nina ci. Muna ci muna hira ya ce,"Jiddazan fada miki wata magana bakinki naki, bana son kowa ya ji."Na ce,"To Baba menene?""An kawo kudin Sadakin ki na gani ina so, da kuma dukiyar aure."Na zaroido, batun kmar cikin mafarki."Da gaske ne Baba?"Ya yi 'yar dariya tare da cewa."Na ta6a miki irin wannan wasan ne Jidda?"A"a

Baba." Na yi shiru ina tunanin wanene wannan zai taimake ni?Ina jin nauyi da na tambayi Baba, sai dai ko wanene kuma ko ya ya yake ina nufin tsoho ko kuturu ne ko kuma Makaho ne kaiko Mahaukaci ne na gode Allah, kuma zan bishi......."Baba ya katse ni da cewa,"Ba ki tambayi ko waneneba."Kaima na kasa na ce,"Ko wanene ma Baba nasan ya yi ne don Allah, kuma ya yi miki albarka.Baba ya ce,"Haka ne, Allah ya yi miki albarka.Kudinnan kuma zan baiwa Maigari ajiyarsukafin isowar Ikcn, sai a saya miki kayan daki dasu.
[29/09 8:48 am] Inna👫👭: IDAN RANA TA FITO 3

4.Murmushi kawai nayi ban ce komai ba. Duk da haka zan so in san ko wanene amma Baba bai fada ba, kamar yasan me nake sakawa sai ya ce,"Duk da ba zan sanar da ke wanene mijin ba, ina mai farin cikin sanar da ke cewa duk kauyan nan da mokatan kauyannan baa ta6a samun mace mafi darajan Sadaki bakamar ki, kai ko cikin birni sai an tona."Ya kama hannuna."Jidda kudin auranki wallahi-wallahini mahaifinki ban ta6a koda ganin kudi masu yawan su ba bare in rike su, naira dubu dari ne cif."Na zaro idanu tare da kankame hannushi."Dubu dari Baba?"Ya jijjina hannuna cikin muryarka kuka."Dubu dari Jidda, talatin Sadakinki, ashirin na gani ina so, hamsin dukiyar aure."Na dafa kirji tare da ajiyar zuciya, hawaye na sauka kan kumatuna."Amma kiyi shiru, wannan tsakanin ni da ke ne, ko 'yan uwana ba zan gaya wa ba.Zan dai je insanar da dangin mahaifiyarki suma kuma zan kwa6e su......."Baba Gaje ta hankado labalen tare da cewa."Ai Hinden tana jiranki ki kakka6e mata shimfida shi ne ki ka zo ban ki ka yi zamanki kuna zagina ko?"Zaraf na mike tare da godiya da Allah da yasa bata ji me muke cewa ba.Ganin takarda da 6awon rake ta zo ta budeledar ta sassana, sannan ta dubi Baba."Allah ya isa in anci da kasanmu."Ni kuma ta zuba mun dankwashi a tsakiyar kai tare da ce min......Like·[image]3·Report·Oct 10, 2014Msmart BG Zee Town*Kuka*Kai antyna kin dai san nafi Haidar ko??tun da niwataran ina ta6a aiki.Ku nayi sututu......Ai Allah ya kara kinayi masu amma aka raina ai ka yanzu an ba parrot aiki da cikawakubari na kara don zata amshe wayartaLike·[image]2·Report·Oct 10, 2014Khadijah AdamuAdd FriendtomLike·Report·Oct 10, 2014MsmartBG Zee Town5."Tsinanniya, ke ce 'yar so saiya saka ki a daki ku ci kifi ku sha rake." Ta hankada ni na fadi sannan na tashi na yi cikin gida.Duk da haka yau sai na samu kaina da rashin jin zafin abinda ta yi min, domin yanzun ina da tabbacin Ikc yana zuwa da zab fita daga wannan halin, dominduk abinda aka sa ma Ikc mai sauki ne, zai zo ya wuce.Na kakka6e mata shimfidar ta kwanta tanata zagina."Shegiya, tuntuni ina jin bacci kin ki zo ki kakka6e min shimfidar.A haka da ki kare mummuna kawai mai kama da naman daji."A cikin zuciyata na ce,"WANNAN KUMA SAI KI GAYA MA UBANGIJIN DA YA HALICCE MU."Ranar dai ban runtsa ba don faran ciki,kwana nayi ina tunani."Gani nake yi kamarin nayi bacci zan farka in ga cewa mafarki ne.Kwana nayi ina nazarin waneneangon nawa?"Amsa daya zuciyata ke bani, ita ce koma wanene Attajiri ne.Ko tsoho ne haka yana nufin zan dan samuhutu.Kai anya kuwa akwai yarinyar da ta kai ni sa'a duk cikin kauyanan?, Ina alfahari da wadannan abubuwan.Na farko duk cewa nafi duk yaran kauyan baki da muni (kamaryadda su Baba Gaje suke fada) kuma ni ce kadai dan Maigari wato Ado ya ta6a buda baki ya ce yana so.Na biyu, ni ce kawai dukcikin kauyannan dan birni da bakon gidan Maigari suka ta6ayiwa magana, sannan duk munin nawa ni ce na fi duk 'yammatan kauyanmu tsadar Sadaki.Lallai mai hkr yana tare da nasara.Washegari ina ta aikina na kosa in fita talladon in je gidan Binto in fesa mata, ko zan 6oye wa kowa batun aurena dole in sanar da Binto, sannan Haja

6.Sai da na gama talla sannan na shiga gidansu Binto, tana zaune tsakar daki nayi sallama na shiga. Sama'ila yana shan kunuya ce,"A'a Kuluwa ce?"Cikin murmushi na ce, "Ni ce kuwa. Binto sannu wai cikin nan naki da girma yake haka ma na Hinde."Ta ca,"Don Allah ke kin cika shirme, zauna mana."Na zauna muka gaisa da Sama'ila, ya miketare da cewa,"Ya tafi Gona."Binto ta yunk'ura zata tashi, ko rakiya zata yi masa? Sai ya ce"Zauna abinki na hutarki.""Allah ya tsare ya bada sa'a."Ta ce mishi.Ya yi murmushi ya ce,"Amin Kuluwa sai anjima."Na ce,"To sai anjima."Binto ta dube ni."Kin san Yaya Ado zai zo hutu kwanan nan kuwa?""Kai! Da gaske?""Allah kuwa." Ta tabbatar min.Ta turo min wani kwano."Ga d'umame nan ki ci ga kuma kunu cikin wancan kwanon shan."Na ce,"To bari in ci, nasan kona koma gidad'an ruwan kokon ma da kyarzan samu tunda Hinde ta zo."Binto ta ce,"Har yau dai abin na Hinde ya k'i ne?"Nace,"To Binto yaushe kuwa lamura zausudai-daita, ko yaushe Baba Gaje tana shiryamata yanda zata ci mutuncin uwar miji da shi kansa miji. Binto ban ta6a rik'e su BabaGaje cikin raina ba ina ga shi ne Allah ya yi min wata sakayya."Ta dube ni da kyau."Wani abunne ya faru?"Na gyara zama na fara kora mata duk yanda muka yida Baba jiya. Murna gurin ta ba a magana.Sep 4Aisha Ummu Shureim Sa'eedMsmart BG Zee Town7."To ya ya ba ki tambayi Baba ba kin ji ko wanene?"Na ce,"Na kula baya so in sani ne, ana shi zaton ba zan yarda ba k'ila tsoho ne."Binto ta ce,"Insha Allahu ma ba tsoho ba ne.""Ni ko nakasashshe ne ma na gode Allah, tunda ya d'aga ni daga gaban Baba Gaje. Sai dai fa Amana na baki bana so ki fada ma wani, don su Baba Gaje ba su sani ba.""Ai ko babu mai ji, sai dai zan so ki fadawaHaja, nasan zata yi murna sosai.""Daga nan can zan nufa."Haka kuwa nayi.Ina shiga dakinta ta tare nida fara'a muka gaisa. Cikin zumudi na shiga karanto mata abubuwan da suka faru. Jin baba bai gaya min ko wanene mijin ba yasa Haja yin shirutare da nuna min bata san komai ba akan auren.San da na ce mata "Ina zaton tsoho ne ko yana da nakasa shi yasa baba ke 6oye minko zan ki.Sai naga Haja ta kwahe da dariya tare da cewa."In Allah ya yarda ma yaro ne."Na ce,"Ko wanene ma Haja in dai Musulmi ne ya yi min.¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤An samu kusan sati 2 da faruwar Imrn, rannan sai ga Dija Aminyar Baba gaje."Ina gibdin murhu ina jiyo su lkcn da take cewa da ita."Kawalli kin ji Ibrn da na samo gidan Hassi?"Ta sake nisawa tare da rik'e bakinta.""In ko haka neGaje kin yi sake."Gaje ta ce "me aka yi kuma? Ko kina nufin batun Hinduwa?"Dija ta gyara zama.""Tabbbas ba ki
[29/09 9:19 am] Inna👫👫: Idan rana tafito

n8.Dariya Baba Gaje tasheke da ita har da kwarewa, sannan ta ce da Dija.""Don Allah ina ki ka samo wannan Ibrn k'anzon kuragen?Ai ko cikin mafarki haka ba zata ta6a faruwa ba, bare gaske."Dija tayi 'yar dry tare da cewa."Ke dai bincika a hankali, domin kuwa za su iya 6oye miki."Cikin rashin yarda da zancen take dariya da cewa"To zan bincika, don ance ba a k'inta mu2m. Amma bisa gaskiya shirme ne wannan zancan." Ta nuno ni da yatsa."Dube ta fa sai ka ce dabbar daji, tayimiki kama da mu2m wadda za a duba ace ana so har ma a aura?"Dija ta shek'e da dry."Wa yaga Mujiya."Da suka fito zata tafi sai ta ce"Tambayar ta mu ji."Baba Gaje kuwa sai cewa ta yi."Kuluwa da gaske aure Babanki zai miki?"Na dube ta sannan na ce,"Yaushe?"Nan suka shek'e da dariya.Dija ta ce,"Har da saurin tambaya taji batun barin gidan nan, babu inda zaki."Baba Gaje ta ce, "Ina kuwa zata, aure sai dai ki ga wasu nayi. Yanzun ma ai kin yi bandaro tunda duk sa'o'inta sun yi aure.Da za su yi sallama ne Dija ta sake jadda

matacewa ta tuhumi Babana. Bba gaje ta ce,"Ki daina damun kanki, "k'arya ce kawai,amma zan tuhumi 'yan uwansa tynda in ya6oye min ba zaya 6oye ma 'yan uwansa ba. ai sune za su bada ta."Suka yi ban kwana ta tafi. Cikin zuciya na ce,"Allah ya shirye ku in madu shiryuwa ne,in kuma ba masu shiryuwa ba ne Allah kai kasan yadda za ka yi dasu.Duk in da Baba Gaje tasan zata samu Ibrn auren nawa ta bincika amma bata samu komai ba, daga k'arshe dai ta tattara ta watsar da batun
9.Cikin satinne sai ga Ado, na sha mamakin ganin yanda Ado ya yi kyau tamkar shima dan birni ne. Har gidanmu yazo yagaida Baba, kuma ya saka wani yaro ya kira ni na fito muka gaisa, na ce,"Ya birni ka gankakuwa Ado?"Ya yi dry tare da kallon jikinsa.""Kemaai kin kusa zama 'yar birni."Da sauri na ce, In ji wa?"ya sassauta murya."Kina nufin za ki 6oye min ne? Ai na samu Ibrn auranki.""A can birnin mijin yake." Nayi saurin tambayar shi.Ya yi 'yar dariya tare da cewa,"Gaskiya kina da sa'a Jidda, duk kauyan nan ke ce ki ka fara samun miji daga birni."Cikin dariya na ce,"Ni fa dan san ko a ina ne mijin yake ba, ban san ma irin shi ba."Ado ya ce,"Za ki san shi, ke dai ki yi ta addu'a Allah zaya dai-daita miki lamuranki."Na ce,"To na gode, ai lamura ma sun somagyaruwa."Baba Gaje ta fito."Kai me ka ke yi gurinta?Ban raba ku ba?"Ya ce,"Na zo ne ai mu gaisa."Tasa bayan hannu ta mauje ni tare fa ce min"Karya kawai, wuce ciki."Ado ya dube ta cikin rashin jin dadin abinda ta yi min."Bana da kin daina nuna hassadar ki da k'iyayyar wannan yarinyar ba ki san irin baiwar da Allah ya yi mata ba, k'ila nan gaba inuwarta zaku sha ke da 'ya'yanki.Nan ko ta shiga jaraba tare da tsine-tsine. Ado ya ce,"Ki dai yi tunani Baba,in babu duniya dai akwai lahira." Ado dai ya manna mata hauka ya tafi.Sai zuma bala'i take duk makota sun taru wai kan me Ado zai ce mata ita da 'ya'yanta za su sha inuwar Kuluwa?"Wacece Kuluwa?"Ko uwarta ma wacece har ta mutu bate ita.Ta gaji ta wuce cikin gidan, nan ko ta shiga jibgata wai ko'ina naje sai in dinga zaginta, sai da ta barni kwance sannan ta ce in zo indebomata ruwa."¤¤¤¤¤¤¤¤Su M.B ana can soyayya ba dama ne, duk wani tattali suna yiwa juna.Tuni kuma sun soma zuwa Makaranta.Sep 4Aisha Ummu Shureim Sa'eedMsmart BG Zee Town10.Basma tana yin duk wani abu da ta san zata faranta masa rai, haka shima. Ta fannin abinci ne yake da matsala, in yana gida ya kanyi irin wanda ya iya suci, in kuwa ba shi da lkc dama suna da masu aiki.Rayuwarsu abin sha'awa, Husna ma ta kiraHjyrta ta shaida mata suna tare da Brotherdin su a America, kuma tuni ta soma zuwa Mkrnt. Nan take Hjyr ta shiga zaginta tare da cewabata da kishin uwa ta nuna maya cewa Bello yafi ta kenan, duk da tozarcin da ya yimata. To ta gaggauta baro shi ta dawo ta yafe ta itama kamar yanda suka yafe Basma.Husna bata katse mahaifiyarta ba sai da takai aya sannan ta ce,"Hjy magana ta gaskiya Brother ba shi da laifi, duk da abubuwan da ku ka mishi bai sa ya ta6a nuna min ba, haka nan bai ta6a min hirar abinda ya faru ba. Hsali ma shi ne ya somamin albishirin cewa yasan va za a tsare ki ba, kuma hakan e ta faru."Hjy ta ce,"Na gode kin dai nuna min cewa Bello ya fini."Ta ce, "Ba haka ba ne Hjy. Dady ba zaya yarda in dawo gurinki ba haka nan zama gidanmu babu dadi tunda ni kadai ce in Dady ya fita.,Sannan kuma Bilal Hjyr sa ta ce ba zaya aur ni ba, saboda abin da kika yi.Ni kuma gaskiya zaman gurin ya ishe ni, ina jin dadi a anan gani ga Anty Basma.,Tsaki Hjyr taja sannan ta ce, "TO shikenan ki zauna ke da makiyan nawa, tundasun fini mahaifiyarku." Ta kashe wayarta."Kuka Husna ta saka, nan Basma ta shiga lallashinta tare da cewa, "Wata rana zata gane, Kuma zata yarda cewa mijina mai gaskiya ne.
[29/09 9:28 am] Inna👬👫: Idan rana tafito

11.Mata da yawa suna bada Ibrn halin maza na rashin kirki ko cin amana, ko kuma sakacin alkawari, niko zan bada Ibrn rike alkawarinshi gami da yafiyarsa.Ki lura Husna, Bello Tahir bai ta6anuna min cewa mahaifina yasa a harbe shi ba, kuma an harbe shin ya yi jinya amma bai nuna min ba, sai da ya taho Sajan yake fada mana tare da ke."Sannan mahaifiyarki'yar uwarta ce dubi abinda ta mishi amma hakan bai sa shi juya baya daga gare mu ba ni da ke.Hasali ma sai tattalinmu gami da nuna kuluwarshi gare mu. Kalli irin kudin da yake kashe mana."Husna ta ce,"A gaskiya Anty Basma kin gama dace shi ne dalilin da yasa ki ka ga ina son Bilal, don wasu da'iun Bros rin nashi ne."Basma ta ce,"Na Allah in yaso sai ki ga ya shirya Imrnkun auri juna.""Allah yasa haka ne."Duk abinda Basma take fadi kan Bello Tahir haka ne, har cikin ranta ta ba shi dukkan gaskiyarta, duk abinda ya ce gare ta gaskiya ne.Ta yi matukar yarda dashi, shi kan shi in yatuna da batun Jidda gabanshi yana matukar faduwa, sai ya samu kanshi da da ya sanin auren da ya dedo ma kanshi, amma kuma in ya tuna da halin Jiddan ke ciki sai yaga cewa taimako ne, fatan shi daya Allah ya shige mishi gaba kan niyarsata alkhairi.Yana cikin mota kan hanyarsa ta dawowa gida Dady ya kira shi yana sanar da shi cewa.""Bello an bani mata, ina nufin shawarar da ka bani nayi kanta. Yanzun haka zuwa ranar Jumma'a zaa daura aure, kuma ta tare."M.B ya ce,"Kai amma fa nayi murna sosai,amma ka bincika sosai ko?"

12.Ya yi 'yar dariya."Na bincika mana Bello, Bazawara ce amma yarinya ce haihuwarta daya, mijintaya rasu ne."M.B ya sake cewa da mahaifin nasa."Ka bincika dalilin mutuwar mijin nata ko?"Saboda cutuka da suka yi yawa yanzun."Ya ce,"Eh hadarin mota ne."Yar limamn anguwar mu ce tana da hankali sosai, hakanan ga duk binciken da nayi bn ji wanda yafadi aibunya ba.""Alhamdulillahi,a gaida mana Anty sai in mun zo."Yana isa gida ya taras da su Basma sun dawo daga Mkrnt, duk kansu suna zube kan kujera. Da sauri Basma ta taso ta rungume shi tare da mishi sannu dazuwa, Husna ta mishi sannu da zuwa. Ya zauna a gajiye ga yunwa.Basma ta zauna kan cinyarshi tana cewa da shi,"Darlingyunwa muke ji sai yanzun Helin ta dora abinci, kaje ka amshe ta don ka fi tasauri kuma naka yafi dadi."Yasa bakinshi ya dan tsotsi le6enta tare da cewa.""Na gajiMy Dear,nima in so samu ne in hau cin abinci yanzun."Dukkansu da Turanci suke magana tun zuwan su k'asar ba sosai suka cika yin Hausa ba."Ta ce,"To kaje ka taya tamana."Ya sake manneta a jikinshi."Basma ke da Husna ya dace ku koyi dafa abincu fa, musamman ke Hunsa in ni na jure baki sani ba ko wanda za ki aura ba zaya jure ba.""To kuwa Brother in ba zaya jure ba sai dai ya yi ta cin Indomie."Dukkan su suka sa dariya."Ya ce,"Na tuna Dady fa ya yi aure."Husna ta zaro idanu.""Aure kuma Bros?""Uhmhm!Ba a dai daura ba sai ranar Jumma'a."Ta ta6a baki, Basma kuma ta ce,"Budurwa?""Yarinya ce amma ta ta6a aure."Husna ta ce, "Ni kam Bros ka ce mishi ya hkr ya dawo da Hjy.,Ganin yadda ta 6ata rai tamkar zata yi kuka sai ya ce,"Tozan shawarce shi amma kin san ba lallai bane ya yarda."Husna ta ce," In ma ba zaya dawo da ita baya hkr da auren ya auro karamar yarinya ta raina mu?"

[29/09 9:29 am] Inna👫👫: 13.Dariya Husna ta bashi, ya dai gano cewa kishi ne ke damun Husna. Waton tana kishin mahaifiyarta."Dady bai isa ya zauna haka ba tukunna batare da wadda zata dafa mishi abinci ba."Ta zum6oro baki."To baga kuku ba?""To in mun yi waya zan fada mishi, ko kuma ki kira shi ma."Ta ce,"A'a kai ne zaka fada masa don ya fu jin maganarka.""To zan fada, ki ka ce in ce mishi kina gaidaAntynmu ko?"Husna ta sake turo baki.Basma tana dry tana kalon fuskar M.B, ta sumbaci wu yanshi tare da cewa.""Honey kana k'ara kunna Husna ko?"Helin ce ta katse su da cewa"Ta shirya musu tebur."Shi kam M.B ya kanci abincin Helin ne kawai don yunwa, amma ba wai don dadi ba, su kuwa su Basma har da

santi.¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤Ranar Juma'a kuwa bayan an tashi daga Sallar Jumma'a aka daura auran Alhj Tahir da Amaryarsa Fatima, wadda aka fi sani daNana, kuma a ranar ne ta tare a gidanta wanda yasha gyara tare da cana dukkan Ma'aikatan gidan.Rayuwa sosai su Dady suka shiga Shimfidawa shi da Nana, lallai namiji damaan ce namjin yana tsufa ta wani gefe ya kuma Ikcn karfinshi ke kara zuwa ya dinga jin shi tamkar saurayi.Nana zata shaida hakan.14.Ni kam ina nan zaman jiran miji har an sa kimanin wata 6 ni da Baba ya ce nan da wata 3 har an kara 3 ga matsi da nake fuskanta daga gurin Baba Gaje fiye da da.Ga Hinde tunda ta haihu aiki ya karu gurina, wankin kashi, goyon yaron mai suna Zubairu, du in da zani dashia baya, ko talla har ma wani Ikcn ya ki uwarsa sai ni.Binto ma ta haihu 'yarta budurwa sunanta Jamila, matar Ado ma tana nan da nata cikin.Shi kuwa M.B baya son zuwa Najeriya ne sbd batun auranshi da Jidda wanda kusan shi ne ya janyo ma kansa, amma in ya yi wani tunani sai yaga kamar bai yiwa iyayanshi da ita kanta yarinyar adalci ba, inya san ba zaya iya ba me ya kai shi cewa za ya yi?"Koda yaushe cikin saka wannan Imr yake, daga karshe ya tattara lamuranshi ya mikasu ga Mahaliccinshi, duk abinda ya faru da shi ya yarda daga Allah ne kuma zai amsheshi hannu bibbiyu

[29/09 9:32 am] Inna👬👫: 15.Cikin haka kwatsam sai gashi aiki ya taso mishi daga gurin aiki an tura shi Najeriya, alissafin shi aikin zai dauke shi tsawon sati 2amma an bashi sati 4, don haka sai ya yi tunanin yin amfani da damar ya cika alkawarin da ya dauka duk da dai Lagos aka tura shi aikinki.#NIGERIA!Ya sauka Najeriya a Abuja, watanshi 9 kenan rabonshi da kasar.Ya sake hawa wani jirgin don zuwa Lagos. Cikin taimakon Ubangijinshi a kwana gomaya kammala aikin shi, ya nufi Kano.Kafin ya bar Lagos din sai da ya hada lefenshi tsaf,a kwatuna ne guda biyar da dan karamin su cikon na shida.Ya bi jirgi ne zuwa Kano sannan ya yi shatar mota zuwa gidansu, kafin ya karaso ne ya kira mahaifinshi ya sanar dashi cewayana shigowa yanzun nan don ya iso Kano din.Dady ba ya gida amma ya kira Nana yashaida mata zuwan dan nasa.Lokacin da yashigo gidan bayan ya sallamimai tasi, 'yan aiki suka kwashi kayansa zuwa ciki.da salla,a ya shiga falon, babu kowa ya sake yin sallma tare da zaunawa kan kujera.Ta fito tana sanye da atamfa 'yar Ingila da bakin hijabi a kanta.Kyakkyawar mace mai cikar mutunci, da fara'a ta tare shi tare da cewa "Kai ne tafe?"Ya yi murmushi."Ni ne Anty."Bata samu matsala ba don bata baringidan babu abinci.

[29/09 11:21 am] Inna👬👫: 16.Nan ko ta shirya masa abinci kan tebur ta zo ta ce"To Bello ga abinci fa sai dai Allah yasa kana cin rin shi domin namu ne na gida."Ya ce,"Anty kenan, ai ni na fi son komai nawa inda zai yiwu in yi amfani da na gidan ba ma abincin ba."Ya ci gaba da cewa,"Ba mu gaisa ba sai batun abinci." Ta ce,"To ai zamu gaisa tunda gida kazo."Tuwo ne na shinkafa da miyar shuwaka, yaci tamkar kar ya koshi don dadi, ya jima baikoshi haka ba. Yana idar da sallah Dadynshi yanashigowa.Ya dubi mahaifin nashi da murmushi cikin tsokana."Dady kai ne kayi k'iba haka?"Dariya suka sa har Nana.Dady ya ce,"Aikin Antunka kenan, cika miniciki take yi da kalolin girkinta."M.B ya ce,"Na lura don nima na shaida haka.""Yaya ya zo babu su Husna?"M.B ya ce,"Ai ya zo Lagos kuma ya kammala aikin.""Allah ya taimaka,ina fata dai ka taho da shirin ka na zuwa kauye, don Babanka Maigari da kansa ya zo kwanaki don jin yanda ake ciki, na kumatabbatar masa da ka iso da sati guda za a soma biki."M.B ya share zufar da ta feso mishi, sannan ya dubi mahaifinsa.""Kayan can lefe da shi na taho."Dady ya ji dadi tareda cewa Allah ya yi masa albarka.Shi kuwa ya ce,"Anty Nana ki duba duk abinda babu sai a zuba, sannan a yi mata dunkunan kayan da za da zai samu duka." Ta ce,"To, sai dai a raba ma

Teloli."Nan ta shiga dubu kayan.Rantsattsun lesuna ne da shaddodi da kuma atamfofi duk na karshen kudi, takalma da gyalulluka zuwa after dress ba a magana.
17.Anty Nana ta yabakaya, sannan ta ce, "Sai kayan shafa zuwa kayan ciki irin su siket." Ya ce,"To Anty sai ku shiga kasuwa, yarinyar dai k'arama ce ina tunanin ba ta wuce sha shida zuwa sha bakwai ba."Anty Nana ta ce, "To za'a siyo. Sai batun dunkunan a dinka duka?""A dinkesu kawai don can ba su da wasu Teloli."Dady ya ce,"Haka ne."Bayan sun gama wannan babin sai Dady ya ce,"Ka sanar da Basma kuwa?""A'a sai nan gaba saboda wasu 'yan dalilai."Haka da dare sundawo daga Sallar Isha'i su da Dadynshi suka samu abinci kusan kala 4, kowanne dai-dai cin mutum uku. Nan fa M.B ya shigaruwan ido ya ma rasa wanne zai ci, nan ya ci wannan ya ci wancan ga kunun aya da kwakwa da dabino, ga so6o.Ya dubi Nana ya ce,"Anty Nana ina ma a nan nake."Duk suka saka dariya.Abinda ya k'ara birge shi da matar mahaifin nasa shi ne, yanda take matukar girmama shi da yin tsantsam da duk wani abu da tasan zai sosa masa rai.Cikin dare yana kwance gefensa na da tunanin Basma yake yi wadda ba su dade da gama waya ba yanzun.Yana son ta bayason abinda zaya sosa ranta. Yana tunanin ranar da zata ji ya sake aure ba tare da ta sani ba.,Gashi ta yarda dashi duk wata gaskiya ta ba shi, tana makutar sonshi.Ya tuna sanda zaya taho, rungume shi tayi tana kuka, kuka sosai da kyar ya sha kanta dama kwana biyu kafin ya taho ya shiga kasuwa da su sun siyi duk wani abu da za su bukata kafin ya dawo., Ya basu mota ya kuma ce baya son suje ko'ina sai Mkrnt, ya tsorata su da cewa kada su ga ba ya nan sucanza dabi'u ya saka abinda duk inda suka je za ya mishi bayani.
18.Duk sun yarda musamman Basma wadda ta tuna abinda ya faru baya. Ya yi murmushi da ya tuna yanda suka tsorata tare da rantse mishi cewa ba za su canza ba.Ya janyo filo ya rungume yana me tuna lallausan jikin Basma tare da kamshinta, kanta ya soma sanin wacece mace, don haka baya wasa da ita. Ma'ana baya son abinsa zai sosa ranta, nashi ganin tafi dukkan wata mace a bayan kasa.Cikin kawana 2 duk wani abu da lefen ke bukata ya kammalu, hatta dinkunan.Ya jinjinawa Anty Nana, don ta tsaya tsayindaka don ganin komai ya hadu.Sajan Sani ne ya ja motar zuwa Garkosukadauki wasu daga dangin mahaifinsa, sannan suka nufi kauyan su Maigari.Gidan Maigari suka sauka, sun ci sun sha sannan suka kuma dunguma zuwa gidan Amarya.¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤¤Ni ina zaunebutu- butu gidin murhu ina yiwa Hinduwa dimamen tuwo, ga danta a bayana yana ta kuka hancinsa dam da majina, sai muka ji tsayuwar motoci.Babana ya fito ya tare su tare da yi musu sannu da zuwa.Sajan ya shaida ma Baba cewa lefena sukakawo, tabarma Baba ya amso nan makotanmu shi da kanshi ya shigo ya same su tsattsayemutan gidan sai kallonsusuke yi.Baba Gaje ce ma ta zo tana baje jayayan hakoranta tana cewa,"Sannunku bayin Allah, daga ina?"Sai kuma ta hango matan Maigari nan taketa nufi gurin su tana cewa,"Lafiya?"A'a wai na ce lafiya?"Kafin su yi magana Baba ya shigo da tabarma nan suka amsa suka shimfida suka zauna
19.Ya ce,"Gaje kawo ma baki ruwa."Da yake bata san dalilin zuwan su ba, nan ta nufi dakin Jama'a don aron kwanon sha, sbd Baba Gaje dai bata da abin kanta.Bayan ta kawo musu ne ta nufo inda ni ke ta zubamin rankwashi iya karfinta har sai da na gigice tare da cewa,"Tashi a nan uwar kallon tsiyakada ki sa su amai da wannan warin naki."Na mike na nufi cikin daki." Daga ciki ina jin Ikcn da matan suka shaida ma su Baba Gaje cewa lefen Jidda suka kawo. Gaje ta fiddo da dukkan idanunta waje tareda cewa," Wacece me wannan sunan, kunanufin Kuluwa?"Suka ce,"Eh."Ta ce,"Kunyi 6atan kai, ina ga dai Kuluwar gidan Me jakai ce."Matan

Maigari suka ce"Ta nan gidan ce ba 6atan kai muka yi ba.",Da saurita iso dakin ta janyo ni zuwa gabbansi."Kun ga fa irin tamu Kuluwar, wane mahaukaci ne zai ce yana sonta?Koko Birni suna matsalar Kuluwa ne ba su da masu sunan.

20.Baba ya yi tsaki sannan ya ce ma bakin "Toan gode muku."Matan Maigari tare da sauran bayin Allah da suka zo tare dai mamaki ya hana kowa magana.Suka mike suka ce,"To su daikan za su tafi."Baba ya kawo kudi ya ba su ya ce,"Ga tukuici."Suka ce ba za su kar6a ba, ya ce,"Su amsa ai haka ake yi, sannan suka amsa.Suna fita nan fa Baba Gaje Faifan bala'i wato ita muguwa ce har da za a dinga 6oyemata abu?"Lallai kuwa za a ja da ita.Yau kam sai ta ji dalilin da za a 6oye mata auran Kuluwa, ko ba ita ce ta haife ta ba ai ita ce taci kashinta ta kuma ci fitsarinta. Saiyau naga fushin Baba inda ya ce,"Karya ki ke Gaje!"Ya bugi kirjinshi "Ni nenan na ci kashin Jidda na ci fitsarinta, ke tauye ta ki ka yi tare da bautar da ita kin manta ne?"Ta ce,"Haka ka ce?""Eh,na fada."In ji Baba.Ta rasa me zata ce, sai ta zari mayafinta ta yi gidan Dija.Tana shiga tarushe da kuka tamkar waddaaka ce mata uwarta ta mutu.Dija ta taso tana sallallami, tana fadin."Kawalli me ya faru?"Cikin kuka riris take sanar da Dija cewa,"Ashe batun auran Kuluwa gaske ne?"Dija ta dafa kirje tare da cewa,"Kai haba?"Gaje ta ce,"Wallahi kuwa, ga lefe can an kawo Adaka ce kusan guda 6 ban ma ta6a ganin irin ta ba."Dija ta ce,"Wanene kuwa mijin?"

21.Gaje ta ce,"Ina zansani?Ni dai ba ruwana da harkar su kayan su ma ba dai dakina ba, kuma ko zan tafi tsirara ba dai su zauna lafiya da mijin ba."Dija tasa hannu ta dafe mata baki tare da cewa,"To sarkin shirme an ce miki ana fadane, batun ki ce ba ruwanki da biki bai ma taso ba, kin san halin kauyan nan ba su iya tsegumi ba.Yanzun a zaga gari da ke ace kina bakin ciki, yi kokari ki danne in yaso 'yan bori na sun ishe su.Za mu sa su turo musu Aljannu su hana su zaman lafiya,ko ya dinga ganinta a Dodo kin gani dole neya sako ta."Gaje ta ce,"Kin kawo shawara, sai dai Allahyasa na iya dannewa, in ga wannan Bakin cikin."Dija ta ce,"Za ki iya mana muje gidan yanun sai ki nuna cewa kin zo ne ki gaya min mu zo muga kaya daga nan sai ki aika duk Jama'a su zo su gani, ki nuna murnarki ki danne komai."Sai ga su sun dawo kafin su dawo ma gidanya soma cika nan kuma aka rasa yanda za a bude akwatuna.Sai da aka aika gidan Maigari sannan aka zo aka bude.Ba Baba Gaje ba, hatta Dija ta ji bakin ciki kayan, gashi matan Maigari sun dawo su ne ke daga kayan saboda sata, dankunne da sarkan ma ba su bari kowa ya ta6a ba, sun dai nuna suka ce daham ne dashi za sutafi.Cikin abin da bai fi sa'a biyar ba Ibrn kayanaurena ya zaga har makotan kauyan sun soma samun Ibr.Wasu da yawa da yawa in za su yi kwatancena kucakar gidan Wanzamai sukece min, shi yasa ba a sha wuya gurin gane ni ba.Dija da Baba Gaje cikin daki suka tara ni sai na gaya musu wanene mijin, na dinga rantsuwa kan cewani ban san shi ba............

[29/09 11:22 am] Inna👬👫: 21.Hinduwa kuwa kuka ta kwana yi wai Baba ya samo min miji a birni ita ya k'i samo mata.Hakan ya k'ara d'aga hankalin Baba Gaje dama akwatunan shagonsa suke kwana ta ce d'akinta ba guri. Sauran matan gida kuwa suna tsoranta.Matar Yaya Auwalu ma har da had'a ni da Allah wai in fad'a mata ko wanene mijin, wallahi ba zata sanar da kowa ba, na ce nima nan bn san shi ba, k'ila ma nakashsshe ne, ta ce haba?"Na ce Allah to in ba haka ba wa ki ka ga zaya aure ni?Nan kuwa matar Auwalu ta je ta sanar da su Baba Gaje cewa mijin nawa nakashasshe ne, wai ta lalla6a ni na gaya mata.Nan kuwa zance ya shiga yad'a gari, kai wasu ma har cewa suka yi K'ila dai irin 'yanshan jinin nan ne da yake ana cewa suna yin amfanin da Mahaukata, to wai ya ganniya zata Mahaukaciya ce.Babana ya tafi ya sanar da

dangin mahaifiyata ya ce da wan mahaifiyata ya dace su zo don kula da kayan aurena da aka kawo, ya dawo kamar yau washe garinsuka zo."A Ikcn Baba ya 6ulo da shagonsa ta cikin gida aka kulle k'ofar waje.Nan dangin mahaifiyata suka zauna, hakanya dad'a k'ona ran Baba Gaje don dai Dija tana tausarta."A na sauran kwana 3 daurin aure Baba Jummalata tsafe min kai, ni kaina na tsorata da irin kwarkwatar da ke zuba dagakaina, kalkashin suka sa suka wanke min kaina sai naji tamkar an cire min kayan nauyin nedaga kan nawa.Ana saura kwana 2 daurin aure Baba yaje suka sayo min kayan d'aki, ranar ce kuma aka saka ni a lalle.23.Gidan k'anwar su Babanmu muke zaman lallan, itama a tsorace ta amshe mu don duk 'yan gefen Baba Gaje ne. Kawaye kuwa har da wadanda ba su ta6a min magana ba, duk sun zo sun shiga bikina. Ban san abokan ango ba bare in dago ko wanene Angon nawa, komai da Angawaye za su baiwa Amare daga gidan Maigari akekawo shi.An saba kajin alibidi guda 2 ake kawowa, sai ga nawa guda 10. Kai komai nawa ya fita daban, ana gobe daurin aure mijin nawa yaaiko da buhunan shinkafa 'yar Gwamnati da Rago tikeke, tun Ikcn aka yanka shi aka shiga suya, miya aka yi ranardaurin aure da safe kuma tyn Asubahi aka girka shinkafa.Wani abin alfahari ba a ta6a yin wani taro a k'auyanmu kamar na aurena ba, ko Ikcn nadin Sauratar Maigari taron bai kai wannnan ba.Motoci daga birni 'yan daurin aure ga su nan.Bayan an daura ne kuma aka shiga cin abinci, suma angawayan sun zo da abincin cikin wani d'an abu ga kuma lemon kwali da na roba.Suka yi ta ba Jama'a kowa sai sambarka dahamdala, mata kuwa ba na kauyan namu ba hatta da na wasu mak'otada kauyan namu sun lodi abinci.Sai dafawaake ana ba Jama'a, ku ce min ina Baba Gaje Ikcn???24.Tana nan daki ta kasa fitowa don damuwa,kawayan ta suna tausarta, in sun fito waje kuma suyita yi mata dariya tare da cin abincinsu gamida kaiwa gidajansu.Dangin uwa ba su da na 2, sune suka tsayatsayin daka a bikin matan gida ma in tana d'aki su fito suma susa hannu in kuma ta fito sai su koma daki.Mutanan k'auyen mu ba su girgiza ba sai da aka gama d'aurin aure suka ga wanene Ango.#MuhammaduBello Tahir,yana sanye da shadda danya ,mai ruwan k'asa 'yar ciki da malun-malun, ya murza hula Minsta itama mai kalar shaddar Haka nan takaliminshi duk in da ya ratsa k'amshine ke tashi.Na ya durkusa gaban su Baba wanda shima ya yi wankan farar shadda malun-malun aska tara itama daga Angon nawa ya kawo masa, ya gaishesu Baba ya gabatar da shi gurin abokansa da wan Mahaifiyata, da kuma sauran 'yan uwansa.Duk sun sha mamaki, da kyar suke iya furta Allah ya sanya alheri.Shi kuwa nanya cika su da kudi, shi da su Ado suka yi masa rakiya zuwa cikin gidanmu don gaida dangin mahaifiyata.Kafin su karaso tuni Ibr ya iso cewa ga Angon nan shigowa, tuni mata suka shiga baza idanu don ganin wanene Angon.Tsohon ne ko nakashasshenne??"25.Lokacin nima ina zaune cikin d'akin da dangin mahaifiyata suke zaune, sanye nake cikin leshi ruwan d'orawa na rufa gyale fari, ni kaina samun kaina da faduwar gaba Ikcn da Sayyada 'yar wan mahaifiyata ta shigo tana cewa wallahi ga Angon ya shigo, mutane suka bisu da kallo ga Marka har cikin gida.Baba Gaje ma tana d'aki hankalinta a tashe son take ta gani wanene Angon?"Suka yi sallama k'ofar dakin da muke, numfashina ya tsaya cak Ikcn da na ji k'amshin turaran dan birni, ban san Ikcn dana yaye gyalen daga fuskata ba ina kallon su.Su uku tsugunne shi da Ado da Sama'ila mijin Binto, idanuna suna tambayar shi cewa shi ne Angon?"Murmushi ya jefa min Ikcn da suka soma gaida 'yan dakin.Ado ya ce,"Ga ma Amaryar tamu ai."Na sake rufe fuska da sauri wasu hawaye ne farin ciki suka shiga bin kumatuna.Ni Kuluwa ni ce matar dan birni, suma ya zube musu kudi sai godiya suke yi tare da shi masa albarka.Al'ajabi dai ya cika su. Baba Gaje kuwa kasa magana

tayi don tsabar firgita, Ikcn da Ado ya nuna mata Angon. Ba ta sanme suke cewa baita bata san ma ya aje kudu sun fita ba, sai da Dija ta girgiza ta sannan ta dawo cikin hayyacinta.Yana fitowa su Hinduwa dama sun ja tungasu da su Laminde suna ta musu kan cewa ko dai Ado ne mijin, don haka suna fitowa Talatu ta ce da Sama'ila."Sama'ila Ado ne Angon?"Tare da Ado suka hada baki gurin cewa,"Ga shi nan."Suka nuna dan birni.Shi kuwa ya dube su tare da cewa da su."Sannunku."Ado ya ce da shi."Yayan Amarya ne."Nan suma ya ciro kudi ya ba su.Cikin sanyin jiki suka amsa zukatansu nazogi,babu kamar Hinde wadda ta kura ma Angon idanu, so take dole sai ta gano makusa a tare dashi amma bata gani ba, don haka ta ja tsaki tare da cewa.""K'ila madan shan jini ne, ban da haka wanene zayakula wannan K'azamar..26.Bayan fitar su haka Jama'a suke ta fadin nayi sa'ar miji, gashi d'an ubansu ga kuma kudi. Ni dai ina aune cikin matsanancin farin ciki ina yi wa Allah godiya. An ce Amarya ko ta buzuzu ce ranar aurenta sai tayi kyau.Ni kaina na yarda da haka, ga kuma k'amshin na musamman sbd turakun da aka fesa min.Kusan k'arfe 2 aka soma jidar kayana zuwagidan dan birni mai Masallaci, nan fa Baba Gaje abin duniya ya bi ya dagule mata dama ko kan kaya sai da suka yi da Baba, ta ce na Hinduwa bai kai nawa kyau ba, gashi ni gadona mai rumfan lamba wanne.Baba ya ce mata Ikcn auran Hinduwa bakya ma sako ni cikin lamuranki, sbd ban dasgi kada ki manta gona ta na saida nakawomiki rabi da kwatar kudin, ke ce ki ka sayo son ranki, don haka kamar ma ki dame ni."Anyi min jere tsaf kowa ya dawo yana yabawa.Da dare kuwa aka zaga da ni dku dakunan gisan mu wai kannan mahaifina da matansu su ti min fada, kowadai sai dai yace to ayi ta hkr Allah ya bada zaman lafiya.Dakin Baba Gaje nan ne karshe.,Kuka ta saka tana cewa, ta yafe min wai in yi biyayya.Na sani kuka bakin ciki ne ta dai wayance ne daga nan kuma sai muka nufi gidan mijina dama Baba shi ya riga ya yi min dukwata nasiha, abunda nake tunawa kowanelkc cikin nasiharsa ita ce kalmar da ya ce shi ba zaya ta6a yafe min ba in har nayi wani abu da ya 6atawa Bello rai, sai dai in bisa kuskure.Ana ta*wake-wake har muka isa gidan, ankunna fitilu gidan ya yi haske.Wasu manyan fitulu ne masu kwai, gidan Maigari ne kawai da irin su.Aka kai ni dakina inda zamu kwana da kawayena da kuma tsohuwa
27.Shayi da beridi aka dafo mana daga gidan Maigari, nasan bani kadai ba da yawan muyawan mu yau ce rana ta farko da muka soma shan shayi.Da rana suka dafo shinkafa da wake. Binto ta yi min kitso gaba daya aka yi budarkai sannan aka gyara min dakin gami da sharegidan, sannan Jama'a suka watse daga ni sai kawayena.Muna zaune sai ga Anguna sun shigo su uku, shi da Ado da kuma Sama'ila. Suka sayi baki da kudi masu dama, kawayena shi kuma ya raka suka tai jiki yana 6ari, sun samukudi shi kuma ya raka su Ado.Ina zaune ina kallon ko'ina na dakin ashe dai zan ga yau?Ashe zan yi aure?Sallamar shi ce ta dawo da ni daga tunanina.Na amsa ya shigo ya tsaya tsakiyar dakin yana kallon jeren.Murmushin yake yi da alama abin ya bashisha'awa."Jidda wannan shi ne me?"Yanuna jeran da hannu."Kwaba ce da jer.""To wannan gadajan guda 2 fa?""Ga naka, wannan kuma nawa."Ya nufi babban gadonmai runfa wanda ya hi katifa, ya kuma gyara ga labulaye.Ya daga labulan yana kallon gadon, ya kalle ni."Ina zan taka in hau?"Na ce,"Ba a taka komai, hawa zaka yi."
[29/09 11:26 am] Inna👬👫: 28.Ya jingina bayan shi sannan ya dafa hannunwanshi guda 2 ya dare kai.Ya jijjiga gadon sannan ya sauka tare da cewa,"Ashe ya zauna da kyau, a zotana zaya dinga lilo."Ya dawo kusa dani ya zauna, ya jawo leda baka."Nasan kina jin yunwa, kici nama kafin muyi krt ko?"Da sauri na ce,"Na k'oshi." Don na tuno Binto ta ce min wai in ya kawo kaza na ci zai ce in biya shi, ya yi min abinda Sama'ilake mata, koda dai ta ce min duk wasu mata da

miji haka suke yi.Yayi-yai na k'i ci, shi kam ya ci tare da wanilemo na kwali ya gama ya ce na yi Isha'i?Na ce,"Eh,na yi."Ya ce,"To in sakko nazauna,shi kuma ya dakko wata ja mai dogon hannu ya dora kan gadon shi ya zuge ta ya ciro jallabiya fara kar da wandonta gajere, ya cire rigar jikinshi ta shadda.......

28.Ya jingina bayan shi sannan ya dafa hannunwanshi guda 2 ya dare kai.Ya jijjiga gadon sannan ya sauka tare da cewa,"Ashe ya zauna da kyau, a zotana zaya dinga lilo."Ya dawo kusa dani ya zauna, ya jawo leda baka."Nasan kina jin yunwa, kici nama kafin muyi krt ko?"Da sauri na ce,"Na k'oshi." Don na tuno Binto ta ce min wai in ya kawo kaza na ci zai ce in biya shi, ya yi min abinda Sama'ilake mata, koda dai ta ce min duk wasu mata da miji haka suke yi.Yayi-yai na k'i ci, shi kam ya ci tare da wanilemo na kwali ya gama ya ce na yi Isha'i?Na ce,"Eh,na yi."Ya ce,"To in sakko nazauna,shi kuma ya dakko wata ja mai dogon hannu ya dora kan gadon shi ya zuge ta ya ciro jallabiya fara kar da wandonta gajere, ya cire rigar jikinshi ta shadda.......

29.Singiletin jikinshi itama fara, na sun kuyar da kaina ban kuma kallonshi ba har ya gama.Ya ciro turare ya feshe dakin tare da ce min an fi so dakin Amarya ya dinga kamshi, cikin akwatunan ki ma akwai turarka kan daki na duba akwatunan akan gadona ta gefe, na ce sai dai da safe ka nuna min su don ni bn san su ba.Ya ce,"To."Ya ce,"Kin san daga yau ni mijinki ne ke kuma matata ce ko?"Na daga kai.""To ya wajaba in san iliminki iyaka inda ki ka tsaya in dora miki kafin nan gaba ki shiga Mkrnt."Na ce,"Ni kasan fa ba wai ina da wani ilimi ba ne.""Amma ki fada min tun farkon yanda baligi zaya yi tsarki har zuwa sallah."Kaina yana kasa ina wasa da yatsan hannuna.""Da farko mutum zaya kama ruwa."Ya ce,"In baya dauke da najasa kenan, kin san ni da tambaya."Na ce,"Meyewannan din?"Ya gyara zama."Kin ta6a yin al'ada?"Na maida kaina kasa na ce,"Eh,amma sau 2 ne kawai."Cikin tsananin kunya da fargaba na fada.""To sanar dani yanda ki ka gyara kanki."Nayi shiru,cikin zuciyata ina cewa,shi kuma dan birni ya soma shige gona da iri.Ya tausasa muryarshi.""Kada ki damu,Musulunci ya yarda da tambayoyin da nake miki, kuma bani da ishasshen Ikcn da zan miki krt mai yawa, sati daya kawai zan yi na koma, sannan kuma zan dauki Ikc ban dawo ba.

30.Na ce,"To ni dai Ikcn da na ga abin sai na tsorata, kamar in sanar da Baba sai kuma sai kumana kasa sbd kunya,shine naje na fada ma Binto, ita ce ta bani wani yankin kyalle ta fada min yanda zan yi, kuma cikin kwana 3n da na dauka ina fama da abin gurin Binto nake zuwa ina gyara jikina da na gama kuma ita ce ta sanar dani kalar wankan da zan yi."Yagyada kai alamar gamsuwa.""Yauwa ko za ki sanar da ni yanda ki ka yi wankan?"Nasakaina cikin gwiwata.""Me yasa ya ka ke sonka sani?"Da sauri ya ce,"Saboda in ji in ba ki sani ba in sanar dake, domin tsarki bayan Imanin dukkan Musulmi to naga shine yasan abinda zaya gyara Ibadarsa."Nayi ajiyar zuciya, sannan na ce da shi."Ni dai haka ta ce min, in yi niyyar wankan da farko sannan sai na daura alwala bayanna kama ruwa, wai so dai-dai."Na kalle shi don jin ko nayi dai-dai."Ya ce,"Ina jin ki."Na ci gaba da cewa,"Wai sai na wanke 6arin damana sannan haguna, a takaice dai in wanke dukkan jikina ya kasance ko'ina ya samu ruwa har gashin kaina, to haka nayi har mata ce min wai Sama'ila ya ce in mutum ya yiwanka mai kyau zaya iya yin sallah ba tare da ya sake yin wata alwala ba?""Haka ne,ita Sallar ya ya ki ke yinta?"Na yi dan murmushi."Haba dai, tun tuni fa na iya Sallah tun ina 'yar kankunuwa Baba ya ke koya min.""Na sani,ina so ne kawai in ji."

Nafada mashi yadda akeyi,sai dai na gaya mishi cewa, lokacin da nake zuwa makaranta izifidaya na iya dana daina kuma sai duk sai na manta wasu. Yace badamuwa zaki

shigamakaranta dolema, sallarki daidai ce sai dai bakya yin zakiri yayin sallarki, yana da kyau ki dinga yin zikirin Allah yanada falala,Allah da kanshi cikin (suratul Bakara) yace," ku anbaceni zan anbaceku, ku gode mini kada ku butulce mini." wata surar kuma yace " yakuwadanda suka yi imani, ku ambaci Allah anbato mai yawa. " Akwai surori da dama da sukayi bayani kan falalar zikiri, manzon Allah (S.A.W) ya bada misalin mai ambatonAllah da marar ambaton Allah kamar matacce ne da rayayye." Batun ya shigeni sosai, nasauke ajiyar zuciya nace dashi"zanso inyi, amma ban iya ba kozaka koya min?32. "kwarai kuwa, amma mastalar dai itacebaki iya karatu kona hausa ba, bare in koya miki a rubuce. Sai dai na sanar dake me saukin fadi a lokacin sallah," Nace "TO. Yace bari in fara miki daga Ruku'u don ta bayan kabbarar harama tanada tsawo, wannan sai a hankali kya rike " inkinyi Ruku'u sai kice ( subhanakalla humma rabbana wabi hamdika, Allahumma gafirlii)suna da dama, amma bari in barki nan inkin dago sai kice ( sami'allahu liman hamidahu, Rabbana walakal hamdu, handan kasiran dayyiban mubarakan fihi) shima mubar wannan donki rikeko?" Nace"Eh. Gamamakin shi sai yaji duk na fada, nace to sujjadafa? Yace "Subhana Rabbiyal a'ala sau uku. Sai zaman tsakanin sujjadar farko data biyu sai kice, "Rabbigifirli! Rabbigifirli!! Ko kice ( Allahummagfirli, warahamnii, wahdini wajburni wa'afini, warzukuni, warfa'ani), kirike wadannan sauran kafin na tafi zan koya mikisu Insha Allahu, koma zaki gyara." yakai karshen maganan yana hamma, nace "to. Nagode"yace, tashi ki saka kayan baccinki ki kwanta nayi shiru ina tunananin ai shima baccin harda kayansa? Yace kin jini? Namike ina ina made tabarma nace" Ai bani dasu" yanufo akwatin ya budesu, ya ciro wasu riguna guda biyu miko min, na amsa sai dai ina tunanin yadda zan sa agabansa, tankar ya fahimta ya dauki buta ya fita, kafin ya dawo tuni harna canza na hau gadona na kwanta. Ya tsaya gaban gadona sai da safe kenan? Nace eh, ya nufigadonsa yana cewa kinyi addu'a ko?' nace yaya zanyi." yasake matsowa daf dani
[30/09 2:08 pm] Inna👬👭: 30.Na ce,"To ni dai lkcn da na ga abin sai na tsorata, kamar in sanar da Baba sai kuma sai kumana kasa sbd kunya,shine naje na fada ma Binto, ita ce ta bani wani yankin kyalle ta fada min yanda zan yi, kuma cikin kwana 3n da na dauka ina fama da abin gurin Binto nake zuwa ina gyara jikina da na gama kuma ita ce ta sanar dani kalar wankan da zan yi."Yagyada kai alamar gamsuwa.""Yauwa ko za ki sanar da ni yanda ki ka yi wankan?"Nasakaina cikin gwiwata.""Me yasa ya ka ke sonka sani?"Da sauri ya ce,"Saboda in ji in ba ki sani ba in sanar dake, domin tsarki bayan Imanin dukkan Musulmi to naga shine yasan abinda zaya gyara Ibadarsa."Nayi ajiyar zuciya, sannan na ce da shi."Ni dai haka ta ce min, in yi niyyar wankan da farko sannan sai na daura alwala bayanna kama ruwa, wai so dai-dai."Na kalle shi don jin ko nayi dai-dai."Ya ce,"Ina jin ki."Na ci gaba da cewa,"Wai sai na wanke 6arin damana sannan haguna, a takaice dai in wanke dukkan jikina ya kasance ko'ina ya samu ruwa har gashin kaina, to haka nayi har mata ce min wai Sama'ila ya ce in mutum ya yiwanka mai kyau zaya iya yin sallah ba tare da ya sake yin wata alwala ba?""
31......Haka ne,ita Sallar ya ya ki ke yinta?"Na yi dan murmushi."Haba dai, tun tuni fa na iya Sallah tun ina 'yar kankunuwa Baba ya ke koya min.""Na sani,ina so ne kawai in ji."Nafada mashi yadda akeyi,sai dai na gaya mishi cewa, lokacin da nake zuwa makaranta izifidaya na iya dana daina kuma sai duk sai na manta wasu. Yace badamuwa zaki shigamakaranta dolema, sallarki daidai ce sai dai bakya yin zakiri yayin sallarki, yana da kyau ki dinga yin zikirin Allah yanada falala,Allah da kanshi cikin (suratul Bakara) yace," ku anbaceni zan anbaceku, ku gode mini kada ku butulce mini." wata surar kuma yace " yakuwadanda suka yi imani, ku ambaci

Allah anbato mai yawa. " Akwai surori da dama da sukayi bayani kan falalar zikiri, manzon Allah (S.A.W) ya bada misalin mai ambatonAllah da marar ambaton Allah kamar matacce ne da rayayye." Batun ya shigeni sosai, nasauke ajiyar zuciya nace dashi"zanso inyi, amma ban iya ba kozaka koya min?
[30/09 2:09 pm] Inna👫👫: 32. "kwarai kuwa, amma mastalar dai itacebaki iya karatu kona hausa ba, bare in koya miki a rubuce. Sai dai na sanar dake me saukin fadi a lokacin sallah," Nace "TO. Yace bari in fara miki daga Ruku'u don ta bayan kabbarar harama tanada tsawo, wannan sai a hankali kya rike " inkinyi Ruku'u sai kice ( subhanakalla humma rabbana wabi hamdika, Allahumma gafirlii)suna da dama, amma bari in barki nan inkin dago sai kice ( sami'allahu liman hamidahu, Rabbana walakal hamdu, handan kasiran dayyiban mubarakan fihi) shima mubar wannan donki rikeko?" Nace"Eh. Gamamakin shi sai yaji duk na fada, nace to sujjadafa? Yace "Subhana Rabbiyal a'ala sau uku. Sai zaman tsakanin sujjadar farko data biyu sai kice, "Rabbigifirli! Rabbigifirli!! Ko kice ( Allahummagfirli, warahamnii, wahdini wajburni wa'afini, warzukuni, warfa'ani), kirike wadannan sauran kafin na tafi zan koya mikisu Insha Allahu, koma zaki gyara." yakai karshen maganan yana hamma, nace "to. Nagode"yace, tashi ki saka kayan baccinki ki kwanta nayi shiru ina tunananin ai shima baccin harda kayansa? Yace kin jini? Namike ina ina made tabarma nace" Ai bani dasu" yanufo akwatin ya budesu, ya ciro wasu riguna guda biyu miko min, na amsa sai dai ina tunanin yadda zan sa agabansa, tankar ya fahimta ya dauki buta ya fita, kafin ya dawo tuni harna canza na hau gadona na kwanta. Ya tsaya gaban gadona sai da safe kenan? Nace eh, ya nufigadonsa yana cewa kinyi addu'a ko?' nace yaya zanyi." yasake matsowa daf dani
33."Kin dai yi addu'a ko?" Na ce,"Ya ya zan yi?" Ya sake matsowadaf da ni."Ki karanta KULHUWALLU, da FALAKI da NASI, cikin tafukan hannunki ki shafe duk jikinki, kiyi haka har sau 3. Sannan ki karanta Ayatul Kursiyyu har zuwa karshenta. Duk wanda ya karantata yayin baccinsa zai kasance yana da wani mai tsaro daga Allah, kuma shaidan ba zai kusance shi ba har gari ya waye. Akwai su da dama amma ki rik'e wannan."Na ce,"To." Na juya na soma karantowa, shimaya nufi gadonsa."Saboda dadin bacci ban san Asubahi tayi ba, sai da ya dawo Masallaci sannan ya tashe ni.Hakika ban ta6a bacci irin na yau ba a rayuwata, lallai dakin kai da dadi yake.Na yi mika yana tsaye kaina ya ce,"Ki ce(Alhamdulillahil lazyahyana ba'ada maa amatanaa wa'ilaihin nushur.) "Na fada ya ce,"To sakko in kullumin kin tashi bacci ki dinga karantawa, ita ce mai saukin fadi cikin addu'o'in bacci, na ce to.Har na kai bakin kofa ya ce,"Nasan dai kin iya ta shiga bandaki da fitowa ko?"Cikin murmushi na ce "(Bismillah) Allahumma inni a'u'zu bika mina khubusi wal khaba'isa, in na fito sai na ce"Gufranaka."Ya ce "Haka ne.""Ado ne ya koya min su."Na zo na yi Sallah yana zaunekan Sallayarshi cikin kayansa ya ciro ta, ya na krtn Kur'ani, dan karami ne irin mai zif din nan, na durkusa gwiwoyina 2 a gabanshi na ce"Ina kwana?"Ya amsa min da fara'arshi."Lafiya lau, mun kwana kalau?
[30/09 2:11 pm] Inna👫👫: 34."Lafiya lau."Na koma na kwanta bacci ya sake yin awon gaba da ni.Lokacin da na farka rana ta 6ullo, na yi mika game da salati, sanna na sakko. Ba yacikin dakin na leko tsakar gida shiru, na dawo na soma da linke kayanshi da ya cirejiya, na sauke jakarshi kasa na dora kayan a kai, sannan na shiga kici-kicn gyaran gadon, ya dan yi babu laifi na maida Jakar kai na gyara nawa gadon sannan na soma shara.Ina cikin sharar tsakar gidan na kusa soro(zaure) sai gashi ya shigo, na tsugunna na ce dashi."Sannu da shigowa."Ya rike kugunshi da hannuwa 2 ya ce,"Yauwa sannu da aiki Amarya, da kin bari nazo na share."Na

dafa kirji tare daware idanuna."Haba dai, wace ni in sanya ka aiki."Yayi murmushi."Da gaske nake."Nagirgiza kai.""Wannan aikina ne."Ya nufi dakiyana cewa,"Allah ya baki lada."Na ajiye tsintsiyar na bishi dakin, kamar yanda dangin mahaifiyata suka fada mini, duk yanda zan dinga yi. Na shiga da sallama, yaamsa na ce "Za'a yi maka waniabu ne?" Ya dan murmusa tare da cewa dani"A'a je ki aikinki."Na gama na kwashe cikin wani danbuhu.Sallamar su Asma'u na ji kannan Binto, su 3 ne duk da kwanuka kansu.Cikin fara'a Asma'u ta ce min.""Amarsu kenan, ga sako in ji Haja.",Na dube ta da mamaki."Haja da kanta?"tayi 'yar dariya."To ita ce ta matsa min mu kawo."Na ce,"To."Sukai dakin.

35.Sun gaishe shi, sarkin kyautar har ya ba su kudi, ya ce "In dauko filat in zuba mishi abincin don ya duba yaga waina ne da kosai da kunun tsamiya, ya ce in zo da kofi.Na zo na aje ya ce zuba min to, na zuba mishi wai ya yi masa yawa in zo mu ci tare.Kunya ta cika nina ce a'a shi kuma ya ce ba zaya ci ba in har bn zo mun ci ba, na ce to bari in zo.Nima na zuba nawa kunun cikin kunya dai nake ci.Bako sallama sai muka ga an banko labule,Hinduwa ce tsaye a kanmu.Yakalle ta ya ce,"Lafiya?"Ta rike baki."Yau ni naga karuwanci, abincin ma tare kuke ci?"Na ce,"Hinduwa lafiya babu ko sallama?""Eh,ban yi sallamar ba don na zo gidanki shi neza ki dinga min jin kai?"Ai wallahi sai na fada wa Baba Gaje.Ya dube ta a fusace."Ke marar hankali, fitar min daga gida. Je kigayawa duk wanda za ki fadama wa, katuwa da ke ba ki iya sallamaba."Ta cije yatsa ta fita fuu...Ya dube ni."Wacece wannan din?"Kaina yana kasa na ce,"Yata ce Hinde, yanzun zata je ne gurin Baba Gaje ta kullanwani sharri.""Kada ki wani damu, ko ta fada me zata miki?"Ai yanzun babu wani umarni ko hani da take dashi a kanki."Na sauke ajiyarzuciya, muka ci gaba da karyawarmu.Ya ce,"Wanke min bandakin can zan yi wanka."
[30/09 2:12 pm] Inna👬👭: 36.Na ce,"To." Da na wanke sai da na kai masa ruwan wankan sannan na sanar dashi, na hada kayan da muka karya na wanke.Cikin sati 1n da dan birni ya yi na karu da abubuwa da dama, musamman ta 6angaren addini, krt kuwa daga Izifi dayan da na iya muka soma sai da na kai nasi, duk na manta ya tuna min tunda ran jiya ya sanar da ni in gari ya waye zai tafi birni, ya kwana 1 sannan ya koma can kasar da yake."Ban yi bacci sosaiba sbd tunaninshi, cikin satin 1n mun shakuduk da ko hannuna baita6a kwatanta rikewa ba, hakan nan mayuka cikin lefena ya zauna ya karantar da ni yanda duk zan yi amfani da su.Ashe turaren dakin ne muka yi ta fesawa nida kawayena a jiki, man shanfo kuma da shi aka min kitso, na kitson kuma shi muka yi ta shafawa a jiki, Allah wadaran rashin sani.Man wanke baki ma da har matar Yaya Auwalu ta ce min wai maganin kasbi ne da kurajan fuska, na ce tunda ban da shi bari na ajiye sai naga me kyasbin na ba shi.A daran duk ya fadan dokokinsa ya ce baya son yawan fita in ba da wani dalili mai karfi ba, shi ma din daga gidanmu sai gidan Haja, na ce,"To, insha Allahu zan kiyaye, amma ina so zan dinga zuwa gurin Binto tana min kitso.""To za ki iya zuwa, kuma mun gama magana da Haka akwai wata 'yar uwarta da ke can wani kauye, ta aika mata zata zota taya ki zama da kuma 'yan aikace-aikace.

37.,Na ce,"To." Ya kawo kudi masu dama ya bani ya ce,"In 6oye sbd cefane ko ciwo ko dai wata lalurar, sannan ga abinci nan cikeda gurin aje abinci, duk irin na gwamnati.Hatta da garin tuwon ma na leda ne, ban iya amfanudashi ba ya dai ce min ba a mishi talge da ruwa ya tafasa takuwa kawai za'ayi.Cikin Satin dayan ma bn ta6a girki ba daga gidanMaigari ake kawo mana. Cikin akwatin ya nuna min guri yace in 6oye kudin don suna da yawa, sai dai na dan ragi wadanda zan rike a hannu.Tun Asubahi ya soma shiri, na kai masa ruwan wanka yaje yayo ni kasa karyawa ma nayi ganin duk na damu ya soma lallashina da cewa kada na damu, duk lkcn

da ya zo zai tafi da ni birni ne gabadaya, ya sani a Mkrnt.Abin maganarsi ta soma tsiwa wadda ya cemin sunanta waya,yana dauka ya canza harshe na tsura mishiidanu una so in san me yake fada, sai dai na lura yana maganane da mutane daban-daban, don wasu yakin kira sunansu sannan kuma da Husna yake magana fa su.Sai dai na lura ya fi magana da wani wai*Mai Diya......Kuma yana yawan ce mishi lobiyu ko da misiyu ne.,Amma na lurako waye yana da mahimmanci a gurinshi, kamar in tambayeshi sai na share kada ya ce na cika tambayoyi....
[30/09 2:16 pm] Inna👫👫: 38. Ya gama magana sannan yace, "To dakko jakar kirakani kofar gidan su haja inda zan shiga mota,"Nace, " za'ayita maganata ace har nafara fita, ya dakko min hijabi ya mika mun sa muje" nasaka ya kulle dakin na daukr mishi jaka yayi yayiinbashi naki, inata jin kunya nuka jera sai dadda kai nakeyi a kofar mai gari duk jama'a sun taruna shige ciki, daki-daki nashiga ina gaida sumaman binto sannan na shiga dakin haja,lale take mun zan zauna kasa kan tabarma tace ina inzo bakin gado in zauna.muka gaisa sai kallonatakeyi cikin farin ciki,tace"Nagode Allah, Hauwa'u kulu keba jinina bace amma jinki nake kamar daya daga cikin jikokina, nasan muhammadu zai kula dake" nayi murmushinace gaskiyanki ne haja yanada kirki" Haja ta gyara zama akwai yar yata mai suna tasalla ta taba yin aiki a birni, itace natura tazo sai ku zauna tare zaki koyi girki gurintadon inda tayi aiki girki takeyi, tanada kirki sai dai tanada fada in antabota kenan, nasan ke zaku zauna Ify gata da aiki" Nace to Insha Allahu zan kula" yayi sallama yashigo na bishi da kalloduk sanda na ganshi nakan rasa dawata kalma zan gode ma Allah, wai dan birnine mijina? Kuma cikin kazanta ya ganni ya aureni, hakika nan duniya banida masoyin daya fishi, ya zauna suka gaisa da haja yana tsokanarta, uwargida zan daga yau mekikeso inmiki kafun intafi" babu komai muhammad aini kagama mun komai tundaka auri hauwa kulu yadubeni yayi murmushi, gatanan kikara kwantar mata da hankali naga duktadamu
39.haja tacd kada kiwani tada hankalinki kinji, aina mata bayanima yau tasalla na nan tafe nasan bakida raini kibata girmanta kinji ko? Nace to su Ado suka shigo, shima cikin shiri tare zasu tafi zai koma makaranta, yace angama wanke motar."nan ya sallamemu rakiya har waje haja ta mishi niko nakasa tashi dan damuwa, sai dai inna tuno yanzu koba komai yanzu na killatu awaje daya kuma matsugunin da babu irinta duk karkararmu.Basujima da tafiyaba binto ta shigo aa amarsu harkin fito"eh mai gidanne yatafi dazun" nan na yini saida azahar lokacin baba tasalla tajima dazuwa har taci abinci, sannan nuka nufi gidan tareda binto don tatayani gyarawa baba tasallagurin kwanciya, saida muka gama tashiga tana sallah sannan muma muka yi alwalanla'asar muka shiga dakina"har yanzu kamshin dan birni yananan adakin tamkar yana ciki sai da mukayi sallah sannan muka zauna hira da Binto tace ke yar gari baki bani labarin yadda kuka kwashe ba daangon nakiba" nadubeta da dan dariya kinsan har yatafi ko hanuna bai rikeba? Nafada miki shifa baruwan shi"Binto tace bawaninna ya dai tausaya mikine sai ya dawo"nimafa danaga ya ragesaura mu biyu a dakin har na soma fargaba, sai na kula sam ba wannan ne agaban shi ba baba tasalla ta katsemu Binto ke bazakiyi girki bane?"zanyi baba yanzu zan tafi, to maza taso kikama hanya kekuma fito muna muyi namu nan mukayi sallama da binto sai nazo kitso haka naci gaba da rayuwata cikin jin dadi harna cika sati biyu agidan, ranarce kuma baba ya kawo mun ziyara nayi murnan ganin shi shima haka ya dauko kudi a aljihun shi wai gashi ragowar sadakinki ne sauran anyi miki sayayya dashi nace nabar mishi yace aa zai saya mun tinkiya wai saina saki acikin gidana nace to. " watarana ina tsaka da

cinabinci shinkafa ce da wake da miya dayakeduk ranar kasuwa baba tasallah ke mana cefane, girkinmu harda nama nakan saka akaiwa haja da babana, amma shi harfada yazo ya mun wai ba izinin mijina nakekai masa abinci in daina bayaso nace babafa yace abinci nane. Baba yace duk dahaka ba kullum ba.
[30/09 2:21 pm] Inna👫👫: 40. Baba gajece nagani tsaye akaina tashigo babu kosallama, gabana ya shiga faduwa ina fadin sannu da zuwa" itako sai kallon dakin take tana kada kai gamida tabe baki' Babu wai dama banda jere harda uwa ta rabe akayi miki? Lallai 'yar s0" tadubi kwanon abincin gabanta lallai dole kikori hinduwa kina cin shinkafa yar gwamnati da nama', bakorarta nayiba, maigidanne yace tadingasallama, Baba tasallatashigo tana cewa"kai kai surutun wanakeji harda zage zage, tadubi baba gaje lfy baiwar Allah? Ban saniba tadubi kuluwa wannanfa daga ina kamar kuncen hauka? Babata ce" nanfa baba gaje ta hau ruwan masifa wai ance mata mahaukaciyanan kuwa tasalla tasoma cewa ance miki mahaukaciya inba mahaukaciya ba mececeke kin shigo wa mutane gida babuko sallama, zoma dai kifita inajin zagin dakike mata ina jinki harda cemata mummuna ke kinga kanki? Nan dai nayi tsuru ina kallonsu,sukayikaca kaca da baba gaje ta shure kwanon abincindake gabana. Tasalla tace tafi dai kina bakin ciki ba kya cin irinshi" sai da ta tafi sannan tasalla take tambayata wacece? Nace mata kishiyar mahaifiyatace, nan dai tayitajinjina rashin hankalin baba gaje. Shi kuma daya kwana gidansa da safe yanufi gidan su dady don yamusu gasuwan ban gajiya da kuma sallama sannan ya daga." ya samu basma da husna lfy sai dai sunyi missin din juna sosai shida matarsa, don haka cikin kwanakin kamar suhadiye juna. Wani sabo tattali gami daji da ita yakeyi, wanda har yasa take jin kanta tamkar babuwata 'ya macen data kaita sa'a a doron duniya, yanzu tagama yadda Mb dinta zai iya zama mata uwa kuma ubanta,daginta kuma miji daya da daya.," Rayuwarsu abin sha'awa Basma tawaniyi kyau kamar balarabiya,MB yakan so ya zauna kawai yana kallonta, kullun kara jinta yake a ranshi bayaso ko daya ya bata mata rai.Aikin shi kuma yana tafiya yadda ya kamata, don haka shima ya goge fiye dada,daka ganshi kasan hutu ya zauna, kwanciyar hankali ya samu guri matsalar daya daya tuno da kasarshi zai tuna da jidda shi kuma baya son damuwar matan shi don hakama ya yanke shawarar kin sanar da ita, ko yaushe suna waya da daddy da kuma anty nana,tare da sauran 'yan uwa da abokan arziki, cikin haka yasamu wata hudu amma ko tuna jidda baya sonyi, duk da cewa yawa-yawan lokaci yana jin tausayinta don haka yakeso yazo yasata a makaranta.
[30/09 3:32 pm] Inna👫👫: 41. Wasa wasa har ana neman acinye wata shida lokacinne aka soma duban watan ramadan, wato watan azumi dady yace mishi suzo gida suyi azumi da sallah,yace dady kayi hakuri sai dai ni inzo inyi koda sati dayane don inada ayyuka sukuma karatu ya dau zafi yanzu" lokacin dayake wayan suna tare da basma ne dady yace sati daya amma kasan kabar matako? Da sauri yamike tsaye don kada lovely wife dinshi taji, yace nasani dady zanzo, suna gama wayan ta kalle shi." sweet heat me me dady yacene? Yazo ya runguneta tare dacewa dady yanaso ne muje muyi sallah agida "tace nima inason zuwa, yace kije kiyime? Tadubi fuskarshi haba dai nida kasata"Aa bayanzuba nidaai zanje saboda su haja inasoma tayi fasfot zan turasu Aikin hajji, Tabe baki tayi bata sake maganaba sai dai cikin ranta tace mayan kauye, shikuma sai yace da ita kinyishiru?' tace to mekake so ince?"Husna ma taso zuwa yahanata musamman ma don taga bilal dinta, suna haduwa ta internet kuma suna waya, ya tabbatar mata mahaifinsa yace sai wadda yakeso zaya aura don haka tarike masa amanar kanta yananan yana jiranta intazo zasuyi aurensu su shimfida rayuwarsu irin wacce suke

wafarki. Nikam tun ina kirga kwanaki har nakoma watanni, inban mantaba wata shida kenan banida wata damuwa don inaci inasha, kowa yaganni sai yace nayi kyau, Binto kawai nakema korafin son ganinnshi.
42.Takan ce min kadana damu ga Ado in ya tafi yana fin haka dadewa amma Aina'u bata damuwa na kan ce to. Amma gara Ado ana samun Ibrnshi, amma ni shiru babu Ibr ko gurin Haja naje sai ta yi ta bani baki.Binto ta ce,"To in ki ka duba fa za ki ga kusan mazan garin nan fin rabi matasan sukan fita neman na kansu, ina nufin rani, saina ce kuma haka ne."A cikin wata 6 nan sau 2 naje gidanmu, bandamu da zuwa ba, don Baba ya kan zo lokaci-lokaci mu gaisa, zuwana na farko Baba ne ya ce nin dan wajan Hinde na fama da k'yanda shi naje dubo shi. Ina ta sallama babu wacce ta amsa duk da cewa suna tsakar gidan su, Jikina ya yi sanyi don na taho da dokin ganin su.Nawa zaton yanzun kowa ya saki na shiga dakin Baba Gaje, Hinde ce zaune kan katifa itama sai ta kauda kai, na ce Hinduwa ashe Zubairu bai ji dadi ba?"Budar bakinta sai cewa ta yi."Kin fi kowa sani tunda ke ce sila.""Za ki gane, garama ki sakar min da."Na mike tsaye tare da cewa."Kin san mi ki ke fada kuwa?"Na fito rai 6ace, na ce"Baba na wuce, Allahya sawwaka."Itama Baba Gajensai naji ta ce,"Lanti kun dai yarda da abindanake fada muku ko?" Gashi daga saka tsakin kukan ciki wuta har ta fice a gidan."Sai yanzun na gane nufin su. Ni ce na kamaZubairu shi ne ina shigowa aka zuba tsakin kuka cikin wuta. Hakan ya zo dai-dai fita saboda abinda Hinduwa ta min.Na yi shiru tsaye a kofar gida, ina cizonyatsa, zuciyata cike da dana sanin zuwa gidan.Na girgiza kai tare da cewa,"Ba komai."Gidan Binto na wuce daga nan zuwana na 2 kuwa rasuwar Zubairu ce najeranar 3 nan ma don Baba Tasalla ta matsa min ne sannan Baba ya zo ce in je i
43.Binto ma ta zo har gida ta ce in tura musu aniyarsu in je, don suna ta yada gare da cewa kin cinye shi shi yasa ki ka ki zuwa gaisuwa, har suna yada cewa mijinki kama shi ki ka yi kika rike mishi kurwa sai da ya aure ki, in ba haka ba me zai ci da ke?"Shi yasa ma tunda ya tafi satin bikin bai dawo ba.Na yi murmushikurum, bn san Ikcn da zasu gane cewa Annabi, ya faku ba. Na ce, to zan je. Shi ne muka je tare da Baba Tasallah. Baba Gaje ce ma ta amsa mana gaisuwa amma Hindesabon kuka ta dasa tare da cewa zan ga karshena."Tasalla ta ce,"In ba taga nata karshen ba aiku kwaga naku." Sai da muka fita sannan Baba Gaje ke cewa nasan bani da gaskiya shi yasa na taso wannan masifaffiyar matar.Kun ji Baba Gaje shege yi da mai zina, sai ka ce itama ba masifaffiyar ba ce, tun dagasannan ban sake zuwa ba.Yau gidan Binto na tafi kitso, na same ta ta yi sanwar dambu, ta ce kin zo da son kananan kitsonku na fama gashi ina aiki, sai ki taya ni."Nan na canza zani muka shiga aiki, na ce mata."Kan sannan ma ya bushe, don na wanke.Ta yarfa min kitsona kanana masu ban sha'awa, na dawo gobe zamu tashi da Azimi cikin birni, su ance sun dauka tun jiya. Na rasa me yasa ba ma dauka Azimi gaba daya, abin yana damuna.Baba Tasalla ta ce,"Zaa siyo cefa ne?"Na ce to, na ciru sauran kudin daritara da hamsin, na cire hamsin din na ce je da su Baba su kenan.Abinda ya samu muyi amfani dashi, ita ce ko aje gurin Haja?Na ce a'a duk da tana tambayata ko ina bukutar wani abu?"Na ce a'a nasan dai tunda da danyan abinci ko ya ya zama sarrafa.
[30/09 3:33 pm] Inna👫👫: 44. Yau Juma'a mun dauki Azimi na 6, na fito daga wanka nayi sallah.Ina zaune ina shafa, na soma kwalliyata don ina son kwalliya.Tasalla ta leko ta dube ni.,"Ke wai ba na ce da ke in ana Azimi ba a wannan fente-fenten ba?""Tashi dai." Na tashi ina kallon fuskata cikinmadubi. Lokuta da yawa in na dubi kaina sai naga tamkar ba ni ba ce, fuskata ta washe ta goge ga laushi, ko yanayin manda nake shafaea ne? Haka nan cikin wata

6n dan nayi a killace jikina ya yi kyau, nayi 'yar kiba kuma kirjina ya ciko." Gashina ya koma kamar na fulani, na kan yi sha'awar kwayar idona farare tar gashin idanuna ya musu runfa.Dama hkrn kana ne da 'yar wushirya man bakin da nakw amfani da shiyasa sun zama farare tamkar kankara, kafufuna sunkoma bani da kaushi yanzun gwanin sha'awa Tiraren da nake shafawa da man da nake amfani da su sun kama jikina har dakina da kayan sawa na kamshin suke yi.Kan gado na hau na baje Akwatuna na ina duba kayan da zan sa, na dago wani jan yadi ina son saka kayan sai dai matsalar riga da siket ne kayan, naja tsaki kusan rabin kayana riga da siket ne.Na zuba musu idanu yanzu haka zan yi asarar kayan nan?Na ciro siket din na sauka nasa bai shiga ba, sai da na cire ciki in juya shi nan in juyashi nan na rasa ta ina ne dai-dai din, siket din sai da kyar.Na dorarigar a fiki na ce sai ku ce ta "yan yaye? Don Allah ga wannan 'yar riga, ga mamakina da saka 'yar shimin da nake sawa cire ta nayi sannan rigar ta zauna na daura dan kwali sannan na gyara kayan, nakuma gyare daki tare da karkade gadonmaigidan, duk da baya nan kullum sai na gyara gadon nasa sau 2, safe da yamma.Haka nan hankicin shi da ya mantada shi duk lkcn da zan yi wanki na kan wanke shi in linke in sa mashi kan gadon.Tasalla ta leko..
45."Ki zo ki kwashe naki abincin, yau dai mun cika kunun nan kiza ki kiran yaron nan ne ya kaiwa Baban naki?"Zan yi magana kenan muka ji sallamar danbirbi.Baba Tasalla ta shiga cewa,"A'a'a lallai yaumuna da manyan baki, da yamman nan kake tafe?"Ni kuma kasa motsi nayi ina kallon san6alelen mijin nawa, wanda ko cikin birni sai sa'a.Yana sanye da kananan kaya wando mai ruwan kasa riga mai ruwan madara.Ya yi 'yar k'iba har da dan tinbi.,Ya yi ado da saje da gashin baki, sam bn san ya zo kusa da ni basai da na ji Tasallahtana cewa so kuwa kai kin tsaya kina kallon shi ba sannu ba barka ya hanya? Kafin nayi magana sai na ji ya hura idanuna k'amshinsa ya gauraye gurin.Na sauke ajiyar zuciya tare da yi mushi sannu da zuwa, ya dubi Tasalla ya ce,"Amaryar ta wace kuwa?"Me ki ke bata ne Tasalla?"Cikin dariya Tasalla ta ce,"Kaji muke ci, ni kuwa sai na amshi Jakar tasa nanufi cikin daki.Ta ci gaba da cewa, sai ka ce tasan kana tafe yau gayan nata yafi na kullum. Ya shigo yana cewa ta ji a jikinta cewa ina tafeko Jidda?Na zauna bakin gadotare da rufe fuska. Yazauna kan kujera na tsugunna a gabnshi nace ina yini?"Ya amsa da lafiya.Sai kallona ya ke yi, ni kuma baki ya ki rufuwa, sam bai 6oye mamakinsa ba har lkcn shan ruwa, dama ya zo da tsaraba ciki har da su lemon zaki da kankana zuwa su Ayaba.Nan Tasalla ta hada su ta yanyanka wai irin yanda suke yi a inda ta yiaiki a birni har ina cewa "Allah yada dai ya ci kada yaga ko kazanta me an hada wannan da wannan sai ko ga mamakina yafi maida kai ga 'ya'yan itatuwan, sai kunu da kosai.,Har lkcn cewa yake ni ce kuwa?Na ganni kuwa?Nan fa dadi ya rufe ni, domin kowace mace na sani ta son mijinta ya yabe ta, ina nufin ta bir ge shi.
46.,Dama Binto koyaushe muke hira takan bani Ibrn yanda zan ju da zaran mun soma rayuwa da mijina. Tun ina gwale ta har na soma kwadaita ma kaina hakan, don Binto irin matannan ne marasa rufi, na kan ce mata ke fa ki ke bani Ibrn cewa Sama'ila yace miki ba kyau ki fadi sirrinku.Tunda ya fiya Sallar Asham bai shigo ba na sake yin wanka na kuma gyara jikina na canza wasuriga da siket din.Na dauki fitila ina dura kalazinr, na gama na gofe gurin. Ya shigo da sallama na amsagami da masa sannu da zuwa ya amshi fitilar hannuna yana haska ni.Yau dai kina son rikita ni da gayunki, ya ce zo ki ji na je ya zame dankwalin kaina."Kitsonki ya yi kyau."Na sunkuyar da kaina gabana yana faduwa.Ya shafa kitson da hannunshi, sai na ji waniyar........... a jikina, donni wani namiji bai ta6a rike ko yatsana ba. Ya ce,"Wacece ta miki

kitso nan haka?"Kaina yana kasa nace,"Binto ce take mun.""Lallai zan yi mata biya na musamman ko?""To dama idan na bata kudi bata amsa, sai dai in Baba Tasalla zata je mana cefane Garko in bata ta siyo mato omo da sabulu na wanke hannu.""Ke ma kin kyauta amma zan yi mata biya."Na dauki dankwalina zan da
[30/09 9:01 pm] Inna👫👫: 47.Na ce,"To." Na koma na zauna a zuciyata kuwa cewa nakeshi kam baya raina abin kallo, ko menene na kallo a kitso?Can na tuna da krtna na ce duk fa krtna da ka koya min na haddace saigobe in ka huta ne zan karanto maka ka ji?"Ya ce,"Eh,amma yau ma da akwai wani sabon darasin da zan fara koya miki, kina so?"Na ce,"Eh,A raina na ce, kila na boko ne. Ya ce,"Yauwa yanzun fara da bani Ibr da bana nan me ya faru?"Na ce"Ba komai."Ya ce,"To ina da ina ki ka je?"Na daga kai alamun ina so in tuno, na ce,"In gana dai fi zuwa gidan su Haja, sai kitso gidanBinto, in kaga na je wani gida sai dai barka ko gaisuwa."Ya ce,"To gidanku fa?"Shi sau 2na ta6a zuwa."Duk na fada mishi yanda muka yi da su Baba Gaje."Yar dariya ya yi tare da cewa dani."Allah ya sauwaka."Amin."Na amsa, sannan na tashi na hau gadona na kwanta shima ya mike ya nufi gadon shi.Na gama karanta addu'a bacci ya soma dibana, na ji yana kirana."Jidda! Jidda!!"Cikin bacci na ce,"Na'am."Ya ce,"Zo ki ji."Na nufi gurinshi.Yana zaune bakin gadon ya ce,"Haka ki ka kwanta ba ki saka kayan bacci ba?"Wadannan za su cutar da ke, cire ki zo ki ji.Na yi hamma sannan na juya na cire na saka, ta kasan gajera ce zan dora ta samanya ce bar ta ma wannan ta ishe ki, bacci nanufi gadona ya ce kin ga zo in koya miki krtn.Na nufi, gurin shi ya ce,"Kin ta6a dana gadon nan kuwa?"Idanuna suka wartsake daga bacci, na ce ainaka ne, ban ankare ba har ya kamo ni ya yi sama dani zuwa kan gadon, gami da ce min.Ya kamata ki dana gadon nan saboda kina hidima da shi.Ba zato sai na jini cikin jikinshi, duk jikana 6ari ya dauka don jin wani bakon lamari........"
48.Ya ce,"Nutsu karatu zan koya miki don shima din yana da mukutar lada."Maimakon in ji yana krtn Aya ko addu'o'i sai naji yana min wasu abubuwa wanda jikina ya kasa dauka, sai dai na kasa cewa ya bari kuma na kasa yunkurin kwacewa.Ban san yaya zan fassara irin wanna sabondarasin da Maigidan nawa ya shiga koya min ba.Ya ce,yana so in kware nan da kwana 3, yana sondukkun abinda ya min nima in masa, bn musu ba ina yi har ma na kan dokanta Ikcn ya yi. Sai dai a ranar cikon kwana 3n ne na gane kuskure na, na zakewa gurin daukar darasin. In da ya tattakura ya maida ni mace sosai.Hakika nasha fama sai dai da ina kuka ya lallashe ni da cewa in yi shiru wai a daran da kyar in da matar da ta kai nisamun lada.Har ma ya sake shigar dani cewa bani ji ana cewa Aljannar mace tana karkashin kafar mijinta ba?Na daga kai, ya ce to ai wannan hanya ita ce babba.Ya share min hawaye wai kada na bari Baba Tasalla ta sani.*
[30/09 9:01 pm] Inna👫👫: 49.Lokacin sahur kasa tashi nayi sai da ya daga ni, ya ce zan iya Azimin? Na ce,"Eh." Shi ne ya amso mana abin sahur tare da ruwan zafi na shan tea da yake ya zo manada kayan tea. Sai da muka gama sahur sannan yaje ya yowanka nima ya ce in je in yi, na kasa tafiya sai Ikcn ya lura da gadon shi da abinda ya faru, wato duk ya 6aci.Lokacin Baba Tasallata yi alwa ta shiga daki, shi da kanshi ya je kicin ya dibo ruwan zafi ya sabi cikin babban baho, sau 3 sannan ya kai min na wanka ya ce in yi irin wankan nan, amma in bambanta niyya.Duk yanda muka yi ta dabaru da kada Baba Tasalla ta gane yake an babba babbane sai da ta gano, ta ce irinwannan tafiya taki Kulu ai gara ki shiga ruwan zafi, shi yasa ya cemin ba ki da lafiya da Asubahi."Shiru na mata yau kuma tun kafin a soma darasin na soma kuka, saida ya lallashe ni da cewa in ana krt ba a maimaitawa ba zaizauna ba, wai in yi hkr. Haka na jure cikin kwananin har wata 'yar rama nayi, yayindaMalamin nawa yake shagalinsa,

sai dai kuma ba a rufe sati 2 ba nima kwakwalwata ta shiga rike darussan nashi masu wahalar fahimta.Cikin Azimin kowa ya ganni yaga Amarya, na dan rame amma nayi haske ji yake yi dani tamkar me? Wannan ya dasa min wani sonsa cikin zuciyata mai tsanani.
50.Wata rana muna kwance wayarsa ta soma kuka, ya daga ya kalli fuskar wayar, wasu haruffa ne guda 4 rubuce jikin wayar tare da lambobi, ya ce min."Yi shiru kada kiyi ko tari."Haka ya kan ce min duk lkcn da muke tare in aka kira shi da wannan lambar. Shirun nayi tamkar in dauke numfashina, ya daga tare da cewa."Honey ya ya ne?Ba ki yi bacci ba?"Bana jin me ake fada daga cikin wayar,sai dai shima tuni ya cana harshe zuwa na boko.Na ciji yatsa don na so in ji shi da wace yake yin waya?Ko don wannan zan soin yi wannan krtn insha Allah.Sun jima sunamagana har na soma bacci, da suka gama wayar na ji lkcn da ya sumbaci wayar. Sai na ji raina ya 6aci, koda ya kashe ina jin shiya jawo ni jikinshi wanda lkcn da zaya yi wayar ba ya yaja da kafa aji shi ne ko menene oho, har lkcn kin motsawa nayi.Ya ce,"Jiddahar kin yi bacci ne?"Na ce,"A'a."Ga mamakin sji sai ya ji na jeho masa tambayar cewa "Kai da wa ku ke magana?",Ya dubi fuskata wadda ya dago da hannuwanshi cikin damuwa ya ce,"Basma ce, kin san ta ko?"Na ce,"Matarka?"Ya ce,"Eh,daga nan ban kumamagana ba, shima bai sake yi min batun basai dai kullum dai-dai wannan lkcn take kiran sa shi kuma ya kirata da Asubahi.Wai har da cewa lkcn su da namu da akwaibambanci, koma menene dai ina jin haushi, don ni in ya tafi ai bana samun Ibrnshi bare ma mu dinga magana ta waya,ba zan iya nuna mishi jin haushina ba ne kawai don yana da wata daraja a gurina.Dafarko ya ce min kafin Salla zai koma, nayi kini-kini da fuska amma ban ce komai ba, daga baya kuma ya ce sai bayan Sallah.A kwana a tashi har sallar ta kusanto, dama da ya zo yasa Sajan ya yo odar siga da geroan rarraba gidanmu har da shinkafa, haka gurin su Haka.
[30/09 9:01 pm] Inna👫👫: 51.Saura sati 1 salla kuma da ya je birni ya dawo, haka ya yi ta rabon zannuwa har da wadanda ba dangi ba in dai da rabo ka zo to zai baka.Lkc hakamata suke yi ta zuwa har ya kare,maza kuma shadda, na Babana dinkakku har da takalmi. Ana jibi Salla kuwa bijimin shanu guda 2 aka yanka daya namu daya kuwa al'ummar Annabi shi yana birni ma lkcn da yasa su Ado suyi ta raba ma duk mai rabo, don haka mijina yana shan addu'a, ni kainamasu tsanata da kyankyamina a da, yanzun so suke su samu shiga gurina, burinkowa ace ta sanniko kuma tana hulda dani.Na aiki me mana shara da aike dan Almajirin Gali na ce yaje gidanmu ya ce Hinde ta zo ta taya ni aiki, wai ni a dole me'yar uwa, don ina sonta da samu.Sai ko Baba Gaje ta ce ya tafi ya gaya min ba zatazo ba, ni boyinta ce?"Hinde kuwa cewa takerenin wayo ne, ni fana sani ita ce da Baba suka yi min asiiri haryau babu wani bazawari da zai nuna yana sona."Baba Gaje ta ce,"To wanene bai san wannan ba?"Ke dai wata shara'ar ba sai a lahira ba,amma ko zan mutu ba mu ci nama ba me zai kai ki zuwa taya ta aiki. Ya zo ya fada min na ce shikenan sai na aika shi ya kira min Asma'u, abin mamaki sai ga matar kanin Babana Laminde muka gaisa ta ce nazo ne in yi godiyar nama da aka aika mana dashi, na ce ba komai sai kuma ta tsugunna bari in taya ku na ga kuna ta aiki, na ce ba takura ko?Ta ce,"A'a ba komai."Baba Tasalla ita ce ta jagoranci aikin har zuwa yamma. Sai gashi ya shigo da kaji gyararru, da kuma wasu manyan ledoji. Natsame hannuna na wanke na bishi dakin, na mishi sannu da zuwa ya amsa da fara'a tare da cewa,"Ya ya aiki?"Na ce da godiya, ya zauna kan kujera naga."Naga aikin ya muku yawa.""Eh,har ma matar kanin Baba ce to zo tana taya mu.""Gashi na karo muku, sai dai ki gobe ma zaku iya yin aikin tunda jibi ne Sallaha
52.Ya zazzago kayan cikin ledar farko wasu shaddodi ne dogayen riguna kala 3, irin masu

maikon nan, daya ja daya ruwan kwai dayar kuma bulu, dukkansu saisheki suke yi, gashi sun sha akin sirfani har da wasu duwatsu a jki, sannan ga yadudduka da atamfofi har da takalma da kuna hijabaiya ce Kayan Sallana ne, ya bada na Baba Tasalla kala 4, itama har da takalmi da hijabi.Da ya fito ta ya ciro kudi ya bawa Laminde ya ce ta sha ruwa. ta yi ta zuba godiya.Da zata tafi Baba Tasalla ta dibar mata nama har ma da dambun naman da Tasallan ta ce muyi.Na yi murna dinkuna, nayi godiya har ma sai da ya ce min ya isa haka.Washe gari kuma muka kara shan aiki har muka ji babu dadi, sai dai mun yi abubuwa irin na 'yan birni.Tasalla ce ta sa aka siyo fulawa muka yi cin-cin, sannan kuma waina zamu yi ranar sallar tun ranar jajibiri muka yi miyar hadawa ya rage.Ranar idi kuwa tun Asubahi muka soma aiki dama a nan Asma'u ta kwana tare da Baba Tasalla.Misalin karfe tara na safe tuni ya gama shirin zuwa Masallaci, Ado ya shigo da sallama in cikin kicin maigida ya kwala minkira, na fito muka gaisa da Ado, ya ce"Sai mun zo girkin Salla, na ce Allah ya kawoka.Na shiga daki, tsayawa nayi ina kallon Maigidan nawa, ya yi kyau fiye da duk tunanin mai tunanin, ya ce ya ya ki ka gani?"Na ce,"Gaskiya kafi koyaushe kyau, Allah ya maimaita mana."Ya ce min,"Kema ina son kafin mu dawo daga Masallaci lallaina same ki kin yi naki gayun." Na ce,"To."Yafito.Ado yana cewa"Suma su Baban sun shirya ai motar zata ishe mu har da su Sulaiman ko?""Zata isa,Garko zamu je ko?"Ado ya ce,"Eh."Har suka fita kallon mijuna nake yi, ya yi matukra kyau cikin yadin mai ruwan madara, kuma hatta agogon shi ruwan madarar ne haka takalimi da hula.
[30/09 9:01 pm] Inna👬👫: 53.Bayan fitar su Asma'u ta ce"Gaskiya maigidan kiyi ya yi kyau."Cikin dan jin dadi na ce, sosai ma kuwa, gashi ya cika mana gidan da kamshin turarensa.Mun zuba abinci da za akai ma Jama'a na gidan su HAJA, don na gidanmu sai na makota, ganin lkc na tafiya na bar musu rabon wainar na nufi bayi donkada ya dawo ya same nu bn iya wankan ba, na zauna zaman kwalliya, sai gashi ya shigo."Ba ki gama ba?"Na ce"Na kusa."Ya dubi fuskata "Zo nan ki gani."Na matsa kusa dashi, ya ce daina yin wadannan dige-digen na kumatunki da goshi, in kin ja girar nan ya isa sai ki shafa kalar kayanki a saman ido, kawo in miki."Ina ta dariya ya cire malun-malun din yasa kan gado, ya gyara min na gira ya shafa min wanu a saman idanu, ni ban ta6ama amfani da wannan din da ya shafa min ba, har da su kumati ya shafa min sannan ya shafa min jan baki. Na yi kyau sosai sannan ya tashi tare da cewa ""Na manta ina tare da su Sulaiman ne yaran kanin Dady Baba Sani, bari in shimfida mana darduma cikin dakin can na karshe."Na ce,"To, dama jiya Asma'u ta share shi."Dardumar da aka sa min a bango dama tuni na cire ta ita ce ya shimfida tabarni ya shimfidata.Jar shadda na saka dama abin ja ya shafa min, na daura dankwali kitsona ya fito wasu sun zuba baya wasu sun zubo an tufke min irin na Barebari, ya ce na kai musu abinci."Nan kuwa na shiga kai musu dama an shirye su cikin dishi tangaran din cikin jerena, Tasallata ce in kwaso a zuba musu.Ado ya ce "Kai yau wannan shirin da aka yi mana in mun ci zai ma ishi kuwa mai gidan?"Fadi yake" Wankan Sallata ya yi." Na fito ina dariya, na koma na kai musu lemunkancikin kwali wadanda dama yazo da su ne
54.Bayan sun gama ya fito ya shiga daki wai za su tafi birni gurin su Dady.Na ce in zo muje? Ya ce a'a muna da yawa sannan zanziyarci abokina.Mun kwana 2 bamu hadu ba to ba su ma san nasake aure ba, don bana son yi ma Basma zanca."Na dube shi da sauri.""Kana nufin bata san ka aure ni ba?Ya ce,"Eh."Yasa hannu cikin aljihu ya ciro bandin din 'yan naira hamsin ya bani.""Ga goron Sallanki."Ya ciro na naira goma-goma ya ce,"Ga kuma wannan ki baiwa 'yan yawon sallah."Na durgusa na amsa ina cewa,"Har haka don Allah?Allah ya saka da alkhairi, sai

kun dawo.""To nawa goron Sallar fa?"Yatambaye ni."Tam, fadi me ka ke so na baka?""Ni nawa sai anjima Ikcn krt sai ki bani."_Na gane nufinshi, sai na yi murmushi.Ya daga girashi guda daya tare da cewa"Understand?"Ban san me yake fadi ba, Iokuta da yawa in zaya min magana sai ya saka boko, ni kobana jin me yake fadi. Ina matukar san bokon nan in iya yaren hannu kaiwa na daga mishi ya fita yana min dariya, yasan anjima zan dame shi da tambayar me ya ce?Tun bayanfitar shi 'yan yawon barka da Salla suke shigowa ina ba su, nan da nan Ibr ya yada gari ina raba sabbbabun kudi yara wasu dayawa ma ban san su ba, har da yaran gidanmu.Nan suka je gida suka kai Ibrn sunzo gurin na basu kudi, yara ma suna ta zuwa ina basu.Nan haushi ya cika su Baba Gaje, ni kama ranar na sake godiwa Allah.*"Hakika IDAN RANA TA FITO TAFIN HANNU BA ZAI TARE TA BA."!!!!
[30/09 9:01 pm] Inna👫👫: 57.Na yi shiru, zuwa can dabara ta fado min na fito naje kicin nadakko fitila na zo dakinna kunna duk suna tsaye. Sannan na fito na kai su dakin su mijina suka ci abinci da rana, na ce su zauna in kawo musu ruwa." Hinduwa ta ce ba shi muka zo sha ba, mun zo ne sbd Babatana son ki bata jari tunda ke kin kasa tunanin hakan."Na ce,"To bari in kawo." Nadubi Baba Gajena ce kamar nawa zan baki?" A fusace ta dube ni "So dai ki ke ki kure ni, to bn ce ko nawa ba in kim ga dama ki bani abinda ki ka yi niyyar har sai kin yi min wani kwaubannen Jaraba? Bar ni in ji da cin mutuncin da mijin ki ya yi mana."Ban ce komai ba na koma daki yanakallona na ciro kudi cikin Jakata na dibi 'yanhamsin-hamsin ba tare da na kirga ba na kai mata, fizga tayi ta kalmashe su sannan ta bangaje ni ta wuce.Hinduwa ma tsaki ta fita,ita dai ta ji takaicin yanda ta ganmu ni da mijinta."Na fita na kashe fitila na maida na koma daki na koma daki na shiga shirin bacci.rannan dai kam na ba da barka da Sallah.Kuyi hrk
58.Washe gari kuma nima na tafi yawon Sallah, sai dai maimakon a bani ce nake badawa. Baba kam da na ba shi kin kar6a ya yi, ya ce dani."Maigidanku ya yi mini komai Jidda, buhun shin kafa da nama, kayan sallar har da kudin barka da sallah, don hakaki bar naki Allah ya yi miki albarka ke da mijinki, da zuri'ar da Allah zai ba ku, ni ai yaron nan ya gama min komai tunda ya aure ki a Ikcnda kowa ya guje ki, ba zan daina horanki da yin biyayya gare shi ba. Na sani ance zomu zauna zo mu sa6a, ina so ki shanye dukwani 6arin rai da zai daga gare shi.Ni kaina ban ce ki gayan matsalarki da shi ba bare wani, in wuta ya hura ya ce ki shiga to ina so ki shiga matsawar ba sa6on Allah za ki yi ba."Na ce,"To Baba, Insha Allah za n yi duk yanda ka ce." Ya ce,"Allah ya yi muku albarka.."Ashe duk hirar da muke yi Baba Gaje tana ji sai da muka yi tace da mu."Su sauran tunda ba kai ka haife su ba ai sai ka ce Allah ya tsine musu.,Babaya ce,"Gaje ina raba ki da la6e, wannan mummunar dabi'a ce."Ta yi cikin gida tana cewa,"Oho dai,sai dai ku hadu ku zage ni din bayan na ba ku da yanda zaku yi da ni,"Eh!Na riga na zama ciwon ido sai hke."Da kallo na bita har ta shigw."Na yi guntun murmushi, Baba Gake kenan,ko sai yaushe za ta gane? Matan gidan mi har zuwa matan Yayanu dari 2, na basu sabbin 'yan naira hamsin-hamsin, Hinde nabata dari uku ganin na ba wa Baba Gaje jiya yausai ban bata ba, nan ta shiga mita da masifa wai don ba ita ce ta haife ni ba shi yasa na ware ta na hana ta don ban bata abin hannuna ba ai ba baya taci, kuma duk hassadata ban isa in ce zan maida ta baya ba."Jikina 6ari na ciro kudin na bata daga nan gidan Binto na nufa Aminiyata, har da sabon yadi na kawo mata cikin kayan aurena ba wanda ban san ba, dama duk damijina ya raba sai da na aika mata da su har da turmin zani.
[30/09 9:01 pm] Inna👫👫: n55.Baba Gaje da 'yarta Hinduwa kuwa taikaicin duniya ne yaishe su, suka shige daki suna takaici.Hinduwa kama kar da kuka, tana yi wa Baba Gaje mitar cewa

ai tuni ta ce zata raba auran Kuluwa amma ta zuba idanu, gashi nan Kuluwar tana ta yin abubuwan da gayya.Baba Gaje ta ce, "Gidan 'yar borinnan zan koma ranar a gabana ta yi maganada Aljanu kuma sun ce za su raba auran, to kin san tunda aka aurar da matsiyaciyar komai na kusuwanci ya tsaya bana sana'arkomai sai dan dashin nan. Kina kallon ko matan gidan nan yanzun sun daina shakkata kamar da, Laminde fa an ce har gidan Kuluwa taje taya ta aiki Basira ke tsegunta min an bata kudi da turmin zani da nama, in da ne ta isa ta ce zata yi min wannan abin?"Hinduwa ta ce,"To ke ma Baba ki je gurin Kuluwar mana ai nasanzata baki kudin in yaso sai ki zo ki kai gidan 'yar borin, in ma da zai yiwu da ni sai in auri mijin Kuluwar ita kuma ta dawo ta ci gaban miki da tallar.",Hinde ta ce," To fadi zamu yi mu ce kin je gidan? Kima bari sai dare sai muje tare nima in samo dan na 6atarwa kafin in maye gurbin ta."Nan BabaGaje ta amince da shawara 'yarta.Wa ya gauwar guzuma, da kwance uwa kwance kan cewa uwar Agwagwa tana baya 'ya'ya sunagaba.Daf da Magrib mijin ya dawo daga birni, kafin sannan na ci uban gayu da watashaddar. Ya yaba sosai, sannan ya shiga Masallaci sai da suka yi Sallar Isha'i, sannan ya shigo na kai masa ruwan wankakamar yanda ya saba, yaje yayo zama ya yi kan kujera wai ya gaji na ciro man sa daga cikin Jakarsa in masa shafa, na tsaya kallon shi ya ce duk fa cikin krtn ne kin ga yi maza ki samu ladan aure.
56.Na dakko ina shafa masa cikin kunya ya juyo dani jikinsa yana min cakulkui, ina kyakyata dariya na makalkale a jikinsa, kawai sai naga mutanea cikin daki sai da suka shigo nema sannan suka ce gafaranku dai, in dai na tsorata makuta don kankamewa nayi ajikinshi.Shi kuma ya ce,"Su wanene ku?"Baba Gaje ce ta yi magana."E,to dama dai mune ashe megidan yana ciki."Lokacin ne dukanmu muka fahimce su wanene, sai kuma na ji kunya na sakko daga jikinshi, su kuwa sunatsaye Hinduwa ta tsura mana idanu.Ya ja tsaki tare da cewa,"Ku jira a waje mana.",Ya ci gaba da cewa,"Ku jira a waje mana."Ya ci gaba da cewa,"Ban son me yasa mutane suke yin abin su tamkar dabbobi ba, sai ka ce ba ku san sallama ba.A tsarin Musulunci in kunyi sallama sai kun nemi izini an ce ku shigo sannan za ku shigo.Na ce,"Kayi hkr ba su za ci kana ciki ba."Ya dada jan tsaki, na fita suna tsaye kowanne zuciyarsa tana suya.Na ce"Sannunku da zuwa."Hindu ta ce "Don mun zo shine Maigidan ki zai wulakanta mu?"Baba Gaje,"Kuma laifina ne daga unguwa muke shine na ce mu shigo amma laifin mune muka zo."Na ce,"Ku jira ya fito sai ku shigo."Suka ta6a baki suka yi shiru.Yakwala min kira naje da sauri ya ce " Kin bar ni ni kadai." Na ce,"Su Baba Gaje fa suna jira ne ka fito su shigo."Ya ce "Kin ga dai kayan bacci nake sawa, Allah ba zan fita bakema je ki sallame su ki zo ki shiga daukar karatu.."
[30/09 9:01 pm] Inna👫👭👫: 59.Na yau ma na bata goran Sallarta itama kudi masu dama. Ranar dai La'sar lis na bar gidan na zo gidan Haja, na dan jima sannan na biyo ta gida na wuce."Anyi Sallah da kwana 3 ya ce min zaitafi fajibi, tun da ya furta zancen ba kasa magana, sannan na hade rai ya ce,"Fushi kike yi?"Na ce "A'a kaina a kasa ya ce to yana ga kin hade rai?"Na dago na dube shi."In ka tafi yaushe ne za ka dawo?"Ya jawo ni jikinshi."Ba zan dade ba."Cikin muryar shagwa6a na ce mishi."Haka kowane lkc ka ke fadi, in ka tafi ba na ko samun lbrn ka, kuma gashi..........." Na yi shiry na kasa karasa zancen saboda nauyinsa da nake ji, ya ce"Uhmhum, ina jikin kuma gashi me ne?"Na ce,"Dama karatun na na ce zai tsaya."Ya dago fuskata ya haska ni da wayarsa."Kina nufin in na tafi ba kya tilawa?""Kai baka gane ba, ba shi bawannan dayan karatun ana tilawa ne."Shima din yayi dariya, sannan ya ce,"Gaskiya shi ba zaya yiwu ba kiyi tilawarsa ke daya ba.""To shi ne ai."Ya yi ta min dariya yana lallashina.Ana gobe zai tafikuwa yaga dun na damu ya ce da ni................

[30/09 9:01 pm] Inna👬👭: Waidama kinasona ne haka natashi zaune nazubawa fuskarsa idanu danbirni kenan to inzan cireson Allah da manzonsa da mahaifana aisai naka nidince dainaga kamar bakaso yatareni dasauri injiwa sonki fadarshi mabata bakine jidda gashi kin hanani komawa gurin aiki nakamo lallausan hannunsa nace dashi abi da dakatafi kake mantawa dani yasake cewa injiwa nikaina bansan lokacin dana jefo masa tambayar cewa ammanasan kafiso matarka daniko Yayi shiru cikin mamaki anya wannan nan gaba baza ayi daru da itaba yanda takebin didiginnan ammasai yace dani aikema matataca jidda dukkan ku so iridaya nakemuku nayi yar ajiyar zuciya nace nayarda da batunka saidai ita tafini kyau nima inason mutum fari yayi dariya kincika shirme jidda kinason fari gashini ba faribane a a nifaba namiji ba macefa zomukwanta au zanbaki albishir ammasai kinbani goro sannan zanfada miki duk wanne goro kakeso nabaka to ke da haja zakuje aikin haji nayi dariya yaukuma da wannan zolayar kazo Allah gaskene nakankameshi saikawai nafashe da kuka dakar ya lallasheni ranar dai kasa barci nayi kwana tunani washegari godiya da addu o i nadingayi masa harsaida yasoma jin haushi yace kada insake masa godiya dokin albishir ya hanani jin haushin tafiyarsa lokacin da namasa rakiya zuwa gidansu haja daga nan zayawuce dama acan motarsa take itama cikin murna tatareni da batun rungumeta nayi itamanashiga kuka yayi tsaki nace ya isahakako nashare hawayena yace sajan zaizo yadaukeku yakaiku cikin birni ayomuku passpot din fita kowacce kasa kilani zandawo daidai da tafiyar ku nan daimukayi bankwana yashiga motarsa yatafi
Haja ce tasanar da mutan gidansu tace jiya da dare yazo yashaida mata murna yan gidan sukayi tatayamu saiyamma nakoma gida wani abin al ajabi saiga zancan yacika gari babana dama nice da kaina nashaida masa shikuma yaja bakinsa yayi shiru dija ce tajiyo zancan tazojikina baritasamu babagaje ke kawalli kinazaune takaici zaikasheki ko tace namekuma keda bakyarabo da kawowa mutum mumunanan labari inaganin wannan inkinbari yakasance kincika wawuya wadda batasan guraran dayake mataciwo ba tagyara zama tareda turo dankwalinta gaba kaikiyi hakuri da labarin da nazomiki dashi dannasan zaikonamikirai gaban babagaje yafadi kadadai tsinanniyar yarinyar nance kuluwa za ada ita birni don inson rantane bataso akaita birni cikin kagara tace kinga dija in bazakifada minba tashiki fitarmin kinzomin da labari bana dadiba sannan kintsaya jamin rai kosai zuciyata tabuga
Dija tace to jingina da bango kafinna fadamiki donkada kifadi tacigaba mijin kuluwa yabiya musu hajji itada baba gaje takatseta da hajji tadafe kirjinta wandatajishi kamar zaifado kasa bakintakuwa kasa furtakomai yayi dija tamike taredacewa zantafi gida inyi sanwa ammaduk mekau narki dolane yatayaki jaje sainaganki dan ashawarta abinyi tafita tanata tuntsira dariya babagaje ma batasan abinda dija kecewaba tashiga tunanin mutum nawanema suka tabazuwa makka aduk fadin kauyan tana tunanin banda gidan maigari babu gidan da suka tabazuwa makka don itacikin dangintama bata tunanin akwauwanda yataba zuwa cikin garin kano ba har itakanta
Lallai dolene tasan abinyi kai Allah ma yasatafarka dagawannan mumunan mafarkin hinduwace ta dafata taredacewa baba lafiya don tajima tanamagana baban batasan tanayiba firgigit babagaje tadubeta baccine yadan saceni har inamafarkin deja tazomin dawani mumunan labari hinduwa tace dija tazomana yanzufa tafita babagaje tadafa kafadarta taredacewa nashiga uku nigaje ceminfatayi kiluwa zaje hajji ko itadawanene manibanji gudanba Hinduwa taza idanu sannan tasakuka taredacewa wallahi nimasainaje hajjifa kikacefa ai wallahi indaibaznjeba saidai

kemakishiga kifita kihanata zuwa
Babagaje tace kwantar da hankalinki inkinso yanzu zanje insamu dija basaigobe ba muje atafkamana rokon Allah tafiyar tafasu kumakiyi shiru kadakibari mugulmatan gidannan suji dannasa cikinsu wasusai sunmana dariya hinduwa tace to abinki da Kauye lungu da sako saidakowa yaji yangidanmuma sunji ammasuna tsoron babagaje laminde cemasaigata waitazo min murna tunkafin mutafi tuni wasu sunfara cemin hajiya kuluwa  muna hirada baba tasalla nace baranaje gidan binto tazano min kaina tunda natsefe kitson sallah tace to bari nima intashi inmana dumame rananayi nadauko man kitsona da sabulun da zanbawa binto nanufi gidan su nashiga da sallama aina u cetana gyara tsakin dambu nace zamuci dambu kenan tadubeni tayatsina baki sannudai nace yauwa inakwana ado yafito cikin fara a yanacewa ran hajiya yadade muna murna fa munji abin arziki nace nagode sainaga tana turo baki araina nace nikinga indai batun adone anwuce gurin binto matayi murna sosai tace Dan Allah sahiba inkinje kisayomin zanin gado insha Allahu zansayo miki wata rana kuwa saiga bakwan gidan maigari muka gaisa yabani waya wai maigida yace inyazo yabani zamuyi magana sannan adaukemu zuwa birni dan yin hoton fita na amsa nakarata akunne kamar yanda nagayakeyi ashe sama akasa nasa kumasai b.
Banaji sosai nadubi sajan saishu kawai nakejifa yace juyane yagyara min saigashi inajiyo muryarshi yanacewa jidda nace na am kanajina yace inajinki nagaidashi sannan yace mushirya za akaimu birni gurin fasfot nace to aimuna shiryawane yace badaiwata matsala ko nace babu
[30/09 9:01 pm] Inna👬👫: Mukayi sallama nandai yakwashe mu sai birni lokaci namatsowa munata shirye shirye duk wani abuda akeyiwa alhazai tuni anyimana dagakan allura harzuwa kan lacca dukbayan yankwanaki sajan yanazuwa yakaimu birni inda akekoyamana yandazamuyi aikin hajji naji haja tanacewa ansamu cigabasosai dakarin ilimi naje binto tayomin kitso litinin saiga sajan wai ankiramu cikin dare zamutashi nanfa mukashiga yin bankwana da jama a munaneman gafara nikam harda kuka babana yace insasu a addu a babagaje kasa fitowa tayi dan damuwa nikam harciki nashiga nayimata bankwana daga itahar hinde basu saurareniba ko ince basu tankaniba kauyannan babu gidan dabasu fitoba sunamin Allah sa ayi asa a sajan yaja mota mukatafi cikin dareko muka shiga jirgi yadaga kafin jirginmu yatashi saida mukayi sallama da maigidana tawayar sajan sayayi shima insakashi cikin addu a Allah yabashi zuri a nagari
